[9/26, 2:34 PM] +234 903 908 6385: Ammi na zaune wuraren 11 tana duba wani littafin azkar while Hawwa na bacci sosai mai nauyin gaske taji kamshi ya daki hancinta mai dadi har saida tadago kanta ta kallo kofa Khaleel ta hango jikin kofan dago kan datayi yasa ya matsa da sauri gefe, shiru Ammi tayi saikuma ta kalli Hawwa dake bacci mai nauyi massage din yamata dadi ga drip ana samata ta lullube mata tundaga ciki har kafafu da bargo daga cikinta zuwa kai abude kanta babu dankwali tayi kyau sosai, she's sure shine yaron jiya shine mijin Hawwa kunya yakeji ne kome? Lallai yaron kam akwai kunya yana abu saikace barawo, Ammi tayi murmushi tana tashi ta taho wajen kofan tabude tafito, Khaleel na tsaye jikin kofan yana sanye da riga da wando masu kyau milk adan hankali yace "good good morning Mom" saikuma yajuya zai tafi dasauri batare daya jira amsan Ammi ba, ahankali Ammi tace "Ibrahim" chak ya tsaya yadan juyo kanshi akasa, dan murmushi kadan tayi tace "bazaka duba matar taka ba? Dan zauna da ita nima kafafuna sunyi tsami bari nadanyi tafiya cikin asibitin kadan" kafin yayi magana ta wuce yabi Ammi da kallo saida yaga tafice sannan yajuyo ya kalli dakin kafin ahankali yabude kofan ya shiga maida kofan yayi yarufe ya tsaya jikin kofan yana kallon Hawwa dake bacci mai nauyi hakanan kawai yaji kirjinshi na bugawa sosai dum dum dum! Gently yadaga kafanshi yataka zuwa gaban gadon ya tsaya tareda folding hannu a kirji yana kallonta, she looks very sick and beautiful a hospital gown din, har lokacin akwai bandage a goshinta but an cire na hannuwanta ga ciwuka a hannu, ahankali yadaga hannunshi yakai gently yadaura

kan left hand dinta wani kalan shock yaji baisan sanda yarike hannun gam ba tareda sauke ijiyan zuciya sannan ahankali yakai yatsanshi yana shafa ciwon hannun wanda yasan Ni'ima ne tamata cus yana mota data tattake mata hannu haka murya chan kasa yace "why will you love a girl this much?" Yabi hannun da kallo that felts super soft kaman hannun little Noor ga nails nata so long and white and clean looks so sexy, mirginowa Hawwa tayi kanta zai fadi daga filo dasauri yakai hannunshi yatare fuskanta yafado cikin palm dinshi tana sauke ijiyan zuciya daya huro a hand nashi cikin muryan bacci tace

"Ammiiii" wani irin lankwasa kai Khaleel yayi yana kallon fuskanta dake cikin hannunshi Her face is so damn soft, baitabajin wani excitement dan mace ta shiga jikinshi ba but right now he's feeling so good, tsareta da idanu yayi yana kallonta ya duko a tsaye fuskanta na cikin hannunshi, kaman mai whispering yace

"Hawwah!" Kar Hawwa tabude idanunta saida gabanshi yayi wani mummunan faduwa yanda take kallonshi da very very bright eyes saikuma tamaida idanun tashiga kullewa suna juyawa, muryan Baba yaji awaje dawani kalan sauri yazare hannunshi fuskan Hawwa ya kife anan kasan filo daidai Baba na bugo sallama yana shigowa tareda Ammi da Ramla dakuma wasu mata guda uku, biyu daga cikinsu goye da yara abaya daya babu yaro abayanta somehow somehow they look like Baba, Ammi ta wuce tana gyara fuskanta, Baba yace "Ibrahima kana nan? Ka kannin matarka Hawwa ku gaisa Khadija" Babban wacce ita kebin Aminu Khadija tace "ina yini Yaya Ibrahim" akunyace Khaleel ya gyadamata kai, Hafsa tace "ina yini Ya Ibrahim yamai jiki" Maryam tace "ina yini ya Ibrahim" Ramla itama tace "Ya Ibrahim ya jikin Ya Hawwa" kaman bai iya magana baisaba da mutane haka ba ana kiranshi Yaya Yaya yace "da...da sauki" yakalli Baba akunyace yace "Baba zan tafi zan dawo anjima" Baba yace "muje na takamaka" shida Baba suka wuce suka fita suna fita Khadija da Hafsat da Maryam da Ramla suka shiga tafi saikuma sukahau rawa, Hafsa tace "wih mijin Ya Hawwa yahadu Wayyoo Allah na I'm so happy for Yaya Hawwa" Ammi tace "kunga karku tadamin yarinya da surutu" duk dariya sukayi sukahau hira.

Around 4 DIG yazo hospital din tareda Abraham da Hayatu Baba yamusu iso suka gaisa sosai, suka ijiye kudi da basket na so many goodies sannan sukama Baba sallama suka tafi.

Shima Aminu around 4 yashigo asibitin Baba yadingamai fada akanme zaibar school yazo....

Wuraren 7 Khaleel yashigo asibitin Salman na binshi da shopping na kayan kwadayi daban daban yarike hannun Noor data isheshi da maganan Hawwa ga teddy a hannunta looking so pretty sukai ciki, tundaga glass na kofan ya hango Hawwa zaune kan gado an ijiyemata table da abinci daban daban kekai Ammi na kaimata abinci abaki tana kaudakai tana yatsine fuska idanunta sun kumbura na kuka da bacci, ga Baba shima tsaye kansu suna fama dataci abinci murya chan kasa Khaleel yace "she's such a child" dasauri Noor tace "Daddy mekace?"

child" dasauri Noor tace "Daddy mekace?"

Kallon Noor yayi baiyi magana ba tace "Daddy let's go inside I want to see FAA" dan ijiyan zuciya ya sauke yasa hannu yayi knocking tareda bude kofan Noor tasaki hannunshi tai ciki da gudu tace "My Fairy Angel Anty" Hawwa tadan bude idanu tana kallonta kawai Noor tahau gadon ta gefen Ammi ta tattaka tafada jikin Hawwa ta rungumeta tsamtsam da karfi

Hawwa itama ta rungumeta yarinyar is freaking

cute and adorable.

Baba yace "Ibrahima shigo ga wuri" yabashi plastic chair shi Baba yakoma kan dogon kujera ya sauna su Salman suna shigo suna ijiye jakunkuna suka fice ahankali Khaleel yace "ina yini Mom" murmushi Ammi tamai tace lafiya lau Ibrahim, aran Hawwa tace "Ammi na ne Mom" da sick eyes tadan kalleshi tana

rungume da Noor tana mamakin meya kawo dan iskan yaron nan asibitin nan taki gaidashi, tasowa daga jikinta Noor tayi tace "FAA ya jiki? That day of accident my Dady was taking me to school I saw wat you were doing" Noor tashiga gwadama

Hawwa, tace "I told my Dady, Dady yafita yadinga bin car naki da gudu he removed you from the car you were biting my Dady hand" tanuna hannun Khaleel dake zaune da sauri yajuyar da hannunshi Baba yace "aiko naga ciwon dama Hawwa ce ta jimaka?" Kin magana

Khaleel yayi, Noor tace "we brought you here FAA are you fine now? U will not fall sick again ko?" Gyadamata kai Hawwa tayi ahankali tace

"yes" dasauri Noor ta rungumeta tace "I love you FAA" tashi Baba yayi cikeda hikima yace

"bari na karbi sako wajen mai keke" Dasauri

Ammi ta tashi tace "muje na bika nafadamai abinda zai fadama Ramla" kawai suka fice.

Itama Noor dasauri tasaki Hawwa ta sauko daga gadon tai wajen Khaleel dake kallonta tace

"Dady I forgot my second teddy in car I brought it for FAA" ahankali yace "meet Salman to take you" dasauri tai wajen kofa tajuyo takalli Hawwa dake binta da kallo tace "FAA I'm coming" Gyadamata kai Hawwa tayi tawuce tafita dakin yarage daga Hawwa sai shi, kafa daya yadaga yadaura kan daya yayi shiru yana kallonta, yanda Hawwa taji ajikinta ana kallonta yasa tadan juyo ta kalleshi hada ido sukayi zata ballamai harara komi daya mata nadawo mata arai, da yanda yayi attempting tabata but yanda taji shiya ceceta, plus dazu Baba nata cewa Ibrahima yakawota asibiti yabiya kudin komi da motocin data bata yasa softly da dan kyar tace "thanks" tadanyi shiru ta dai daure tasaki muryanta tace

"thank you for saving my life" tasakeyin shiru ahankali tace "once nakoma aiki i will find a way to pay you back every penny daka kashe" tasakeyin shiru chan tace "all this daka kawo kasa atafi dasu banso, i hate favors barinma na mutane like you! So I will pay back everything" Murmushi kadan yayi batare dayayi magana ba wato tana sick bed still masifa take, Noor tadawo dakin ta tafi wajenta da sauri tabata teddy tace "FAA take, Dady said you will soon move to our house kikazo i will give you more and more teddy kinji" dan murmushi kadan Hawwa tamata tace "thank you beautiful Noor" tana mamaki uban me zai sake kaita gidansu dayake gayama yarsa zata" kusan 10mins yayi sannan yakalli Noor daketa zuba yace "let's go" kiss ta manna ma Hawea tace "bye FAA" murmushi sosai Hawwa tayi tace "bye Noori" wucewa tayi wajen Khaleel yarike mata hannu sukai wajen kofa hakanan Hawwa samin kanta da kallonshi tayi, the way he walks, he way he held Noor's hand, everything looks soo....ta tsaida tunanin, saida yakai daidai kofa ya tsaya Noor ta fita dan juyo da kanshi yayi karaf suka hada ido dasauri Hawwa ta dauke kanta, cikin dan iskan murya Khaleel yace "see you soon cry cry Kulu" dawani irin sauri Hawwa tajuyo ta kalleshi kaman zakanya, gira daya yadaga mata yace "see you very very soon Kululu" kawai yasa kai yafice daga dakin Hawwa tawani yunkuro tace "sunana Hawwa not Kulu or kulul whatever" Khaleel na jinta yayi murmushi yawuce abinsa.

Yau Hawwa ta tashi da karfinta sosai tun asuba Dr yazo yace "za'a sallameta yau but sai Ogansu Mai asibitin yazo" aka cirematata bandage na goshi da hannuwa ciwukan sun warke tanada jiki mai kyau sosai,

wanka tayi tasa wani simple gown da aka kawo mata na atampa red dayamata kyau sosai, ta rame idanunta kana gani zai nuna maka tayi ciwo but takara kyau skin nata sai glowing yake na drip datasha, tun wajajen 7 Aminu yazo dan daga masallaci yazo basai Baba yazo ba daya shigo dakin Ammi bata ciki taje karbo magunguna daga pharmacy sai Hawwa dake zaune ta kishingida hannunta rikeda wayanta tana dannawa tana replying messages na DIG dasu Hayatu, ganinshi yasa ta dago kanta dasauri yayi wajen gadon yana murmushi yace "ya karfin jiki Ya Hawwa?" Murmushi kadan tamai tace "Alhamdulillah I'm fine yaushe zaka koma school why did you even come back"? Zama yayi gefenta yace "yayata that is the strongest person I know a duniyan nan tana rashin lafiya why won't I come?" Shiru Hawwa tayi tana kallonshi tadan harareshi kadan tace "mutum sai dadin baki" dan dariya yayi yace "Ya Hawwa nasha fruits dinnan"? Gyadamai kai tayi yadauka da sauri yana sha Ammi tashigo tace "Aminu jinya kazo ko cin dadi jiyafa haka komi kuka raba naka yamafi na su Khadija" murmushi yayi yace "Ammi to nine babba" hararanshi Ammi tayi ta ijiye magungunan tace

"maza gamaci mu hada komi Dr na zuwa za'a sallamemu wai" tai maganan tana mikawa

Hawwa red veil nata Hawwa tasa hannu ta karba tayafa saman kanta daba dankwali, duk suna zaune har wajajen 9 wayan Hawwa dake hannun Aminu yana connecting hotspat nata danashi  Aminu yana connecting hotspot nata danashi yahau ringing dasauri yabata wayan yace

"Abraham office" hannu tasa ta karba tana kwanciya ta danna wayan tana sawa a speaker daidai lokain ana knocking tareda turo kofan Abraham yace "Hello Miss Hawwa how are you feeling" magana kasa fita yayi daga bakin

Hawwa sabida Khaleel data gani ya shigo yana sanye da labcoat ajikinshi an rubuta Dr Khaleel Mangal, ga stethoscope a wuyanshi hannunshi rike da file na Hawwa dakuma office pad da pen idanunshi kyar akanta ga Dr daya saba duba Hawwan tareda shi sai Nurses guda uku daidai Abraham yasake cewa "Hello Hawwa are you there?" Firgigit Hawwa tadan farga daga kallon Khaleel, adan rude tace "uhn" Aminu yasauka dagakan gadon cikeda murmushi yace

"sannunku ina kwnan ku" gyadamai kai Khaleel yayi kanshi akasa yace "good morning Mom" kafin ta amsa yayi wajen gadon daidai lokacin Abraham yace "huhh wat a relief! I'm so glad you're okay l've been so worri....." wayan Khaleel yasa hannu ya dauka tareda katsewa Aminu yadaura hannu a bakinshi yana makale dariya Ammi tadanyi murmushi kadan tace

"muje waje Aminu" suka wuce suka fita, wani kalan kallo Hawwa tama Khaleel irin who gave you the authority to end my call amman mutanen data gani wajen yasa tadaure tadauke kai batai magana ba, professionally Khaleel yace

"can I have your hand Mrs Lee?" Wani kallo

Hawwa tamai shekeke irin is something wrong with this guys head, dayan Dr yace "Dr Khaleel she's the patient I consulted you for kace nakara mata dosage na wannan medication din nan and BP ya sauka sosai" "hand" Khaleel yafadi yanda zata bama dan iskan nan hannu da kyar kaman ta kurma ihu ta bashi hannun tadauke kai tana kallon gefe, daura mata abun auna BP Khaleel yashiga yi sannan ya makala

stethoscope a kunne da gangan yawani zauna abakin gadon yana facing nata arude tajuyo zatai magana yace "shiii idan ana auna BP ba'a magana" hadiye maganan Hawwa tayi wannan wani irin mutum ne, pulse nata da heartbeat ya saurara sannan ya zare stethoscope din yakalli Dr yace "she's good" yakalli Hawwa yace "any complain Mrs Lee"? Dauke Kai tayi tareda girgiza mai kai bataso ta disgashi gaban abokan aikinshi ganin he's not jobless ashema yayi school, gyadakai Khaleel yayi yace "in that case I can discharge you" yashiga rubuce rubuce a iPad din da pen sannan yabama Dr yace "zaku iya tafiya" wucewa sukayi suka fice saida Hawwa taji an rufe kofan sannan tajuyo hada idanu sukayi yana mata dan iskan kallo azuciye tace "katashi daga kusadani" cikeda kakkausan murya yace "anki" iyyee wow just wow irin kallon da Hawwa kemai kenan ganin karfin halinshi, rage murya sosai yayi yace "idan kika kara kuka kika sa kanki damuwa BP ki yatashi sabida that mad, crazy, babaric woman of yours mai kama da gumakan Egypt mesuem I will reap your heart off your chest kimutu gabaki daya nayi donating all organs naki to mabukata, starting from heart, liver, kidneys with this eyes etc" wani irin kallo Hawwa kemai baki bude ikon Allah, tadaure tarufe bakin tace "you're nobody in my life dazakamin detecting what I should do and what I shouldn't, you're nobody to me Pops boy!" the way she talks shit! he can't even explain but he enjoys it, dan matso da fuskanshi explain but he enjoys it, dan matso da fuskanshi dab da nata yayi dasauri takoma baya gabanta na faduwa sanin su Ammi na waje tace

"me..me....mehaka?" Ahankali Khaleel yace "I want to actually shows you who I'm in your life" dasauri yakawo fuskanshi kaman zai mata kiss Hawwa batasan sanda ta mika duka hannayenta biyu ta daura a kirjinshi ba hakan yasa ya tsaya chak kirjinshi ya buga dum! Hawwa tace "is this abinda ku kema patient naku a hospital dinnan?

I will sue you Allah" dan murmushi yayi cikeda tsokana yace "koni i will sue you for touching my chest, index finger naki on my breast kina tabawa!" Abala'in haukacewan sauri Hawwa ta janye hannunta dagakan kirjinshi jikinta yahau rawa tama kasa magana, she just hates dan iskan yaron nan, did he say breast uban wani breast zata taba ajikinshi? Murya chan chan kasa Khaleel yace "do you have crush on me?

Cus you were trying to take advantage of your handsome Dr duk kin gama mammatse mini this" yataba nonuwansa yana mata very cute smile da white hakoranshi ke showing yamata wani irin kyau a idanu.

Bugawa kirjin Hawwa yayi sabida yanda murmushi taga yamai kyau da sauri ta dauke kanta tayi folding hannuwanta a kirji tace "ewww

Allah ya kyauta you don't even belongs to league na men da Hawwa fancy, babu abinda zanyi da womanizer, drunkard and a playboy like you!" Shiru Khaleel yayi yana kallonta kaman mai nazarin wani abu saikuma yatashi daga bakin gadon jakan daya gani a tsakar dakin yadauka yace "we will see about that if this womanizer, drunkard and what's even the last one dakika fadi Kulu"? Aharzuke Hawwa tace "nace maka ba sunana Kulu ba" dan murmushi kadan yayi baice komiba yawuce kofa, Hawwa data kara kulewa sabida yanda taga ya maidata mahaukaciya tace "ina zaka da jakana? Zaka kara da sata akan qualities din naka ne"?

Tsayawa yayi saikuma ya juyo ya kalleta yabude baki zaiyi wata magana kawai saiya daga mata gira daya yamata dan iskan murmushi yabude kofa yafito dasauri Aminu yazo zai karbi jakan yace "kawo Ya Ibrahim nadauka"girgizamai kai

Khaleel yayi yace "no dauko sauran saika sameni a mota awaje" yawuce Ammi tabishi da kallo kawai taji yafara kwanta mata arai itama ta tashi tashiga dakin Aminu ya kwaso sauran kayan yafito, Ammi takalli Hawwa data kirne fuska tace

"lafiya naga ranki abace" dasauri ta gyara fuskanta tace "bakomi Ammi" hannu Ammi tamika mata tace "tashi mutafi gida to" ahankali ta sauko daga gadon Ammi narike da hannunta suka fito Khaleel na tsaye tareda Aminu yagansu sun fito duk yanda yaso yadena kallon Hawwa data haderai tadauke kai yakasa daga Ammi har

Aminu saida sukaga kalan kallon da yakema

Hawwa kaman zai hadiyeta da idanu, har wajen motan sukazo Hawwa tace "ina keken Aminu"?

Dan sosakai Aminu yayi zaiyi magana Khaleel yace "I'm taking you home dakaina" yasa hannu yabude musu bayan mota yace "Mom shiga" ahankali Ammi ta shiga shikuma Aminu ya zagaye shiga gaba abinshi Hawwa ta kalli

Khaleel da idanunta dahar sunyi ja, Ammi ta leko ta window ganin yanda take hararan Khaleel tace "shigo mana Hawwa" danne komi tayi sabida Ammi ta shiga taki rufo kofan yadanyi murmushi yasa hannu yarufe yashiga gaba ya kunna motan he can't even remembers d last time dayayi driving haka yaja motan su Salman na binsu abaya cikin wata Lexus.

Aminu sai hira yakema Khaleel, adan hankali yace "me kake karantawa a school" Dasauri yace "computer science engineering but nagama project nakeyi" gyadamai kai Khaleel yayi baisan kodan shi baida siblings bane but he kind of love siblings nata barinma yanda yaga suna sonta and suna sonshi ahaka har gida parking yayi Hawwa tabude tafito azuciye Baba yace "oyoyo oyoyo" kawai ya rungumeta yace

"mara lafiya yaya jikin eh patient" dan murmushi tama Baba yace "naji sauki" da gudu Ramlat tafito tana zuwa tai wajen Khaleel tace "Ya Khaleel oyoyooo sannu da zuwa good morning" kallon Ramla yayi kowama na wajen yayi saikuma yayi murmushi, sosai Hawwa ta tsare shi da idanu he looks so good dayana murmushin, he just loves yanda suka nuna suna sonshi, cikeda wasa yace "Ram......" dasauri tace

"Ramla sunana" gyadamata kai yayi yace "nice name" zatai magana Ammi tace "ke kibar mutane su huta" Baba yace "zoka zauna

Ibrahima" dasauri Hawwa tasaki hannun Baba tawuce ciki abinta su Ammi da Ramla suka bita sai Baba da Aminu suka zauna awajen, Baba ya kalli Khaleel yace "sannu da kokari Ibrahima

Allah yabaka lada nagode da komi" dan sauke kamshi kasa yayi Baba yace "yau zan sanar da Hawwa zancen auren ku" ahankali yace

"Ibrahima Hawwa matarka ce yanzu kaine keda iko da ita bani ba, Alhamdulillah tasami Ipy an salla mota daga asibiti ko yanzu kace zaka tafi da ita ban isa nace a'a ba" Baba yasake shiru yace "inaso ka sanar dani yaushe kakeso ta tare? Kanaso ayi taro ne? Zanso na gayyaci yan uwan marigayiya mahaifiyarta dake kauye da nawa yan uwan, yanda akai auren mudan sanar da mutane bikin suzo wannan shine ra'ayi ma amman kai me kakeso?" Shiru Khaleel yayi baitaba biki ba as far as public is concerned haryau anamai kallon mara aure ne dan ba'a taba sanar da bikinshi waje ba, hakanan kuma ya kalli Baba ya kalli siblings nata kawai sai yaji he wants to throw wedding for them, sister su batai aure da wuri ba is only right he lets them celebrate her, and one last final point is kodan ya kular da Hawwan yanuna mata he can actually get duk kalan macen dayakeso yasamu aduniya yanaso yayi biki ayi su dinner yayi kissing nata in public yatabata bayanda zatayi, wani, Kayataccen murmushi yayi yace "Baba inaso ayi biki, nan da 3weeks" Dasauri Baba yace "dubamana date Aminu" calendar Aminu yashiga yana duba date yace "July 24th kenan

Baba ranan asabar" ahankali yace "Baba I will handle everything zan kawo katin biki da komi"

yakalli Aminu yace "kome akeso kamin

message" Dasauri Aminu yace "banda number ka" kiramai number shi Khaleel yayi yayi saving sannan yatashi yace "Baba natafi" Baba yamai murmushi yace "bye my son".

EPISODE

4

Sosai Hawwa ke masifa aranta tana shiga cikin gidan, menene business din yaron nan da gidansu? She don't understand sun masan wayeshi kuwa, tana shiga gidan Umma tagani a tsakar gida tana gyara hatsi tana ganin Hawwa ta dauke kai Hawwa tawuce dakinta batare datace mata ci kanki ba, dakin kamshi Ramla tasaka turaren wuta, kwanciya tayi akan gado ahankali, Ammi tashigo tace "mezakici nadafa miki Hawwa?"Ahankali tadaura kanta kan cinyan Ammi tai shiru batamasan me bakinta keso ba, Ammi tace "bari zanje kasuwa sainamiki farfesu" gyadama Ammi kai tayi tace "Ammi kidauki ATM card dina akwai kudi" dan gyadamata kai Ammi tayi Ramla na shigowa dakin, Ammi tace "Ramla zauna da yayarki kome takeso kimata, bari natasa Aminu gaba muje kasuwa tare muyi cefane zan taho da flask ma asaka ruwan zafi banso daga yanzu kuna zagawa da ruwan sanyi kinjina baida kyau ma mace" gyadamata kai Hawwa tayi Ammi tadauki jakan Hawwan tazare ATM dan bawani kudin kirki takedashi ba, tanaso tasaima yarinyar abubuwa da yawa tace "natafi" atare sukace "saita dawo" tafice tna fitowa waje taga Baba da Aminu na magana dasauri Baba yadakata yace "Zainabu ina zaki"? Anatse tace

"wai kasuwa zani Malam nadanyo cefane Hawwa tace zatasha farfesu kasan har yanzu bata iyacin abinci sosai, Aminu tashi muje ka kaini" dasauri Baba yamike yana rage murya yace "inataso muzauna muyi magana Zainab, to mutanen sun samin miliyan hamsin din sadakin Hawwa a account an bani gwalagwalan kuma amman na adanasu, kece mahaifiyar Hawwa inaso na zauna dake da ita mubata sadakin daganan sai mu karbi abinda ba'a rasaba mu mata kayan daki kekuma kiyi naki shirin kinfini sani dai" gadamai kai Ammi tayi tace "ba matsala Malam yau zamuyi maganan da daddare In sha Allah,

Aminu tashi muje" tashi Aminu yayi daidai su Khadija na zuwa sunma Hawwa girki Baba ya dakatar dasu yace "ban kuma ce naji wani ya sanar da Hawwa zancen nan ba"

Wucewa Ammi sukayi kasuwan, sun sayi kan rago, dadan yan abubuwan datakeso tama Hawwa girki dasu sannan tasiyo mata babban flask na ruwan zafi suna dawowa taga Hawwa ma na bacci tashiga girki Umma sai bambami take yanda yaran ta ke dakin Hawwa wlh suka shareta wajajen 3 Ammi tagama girkin sosai Hawwa taci takoshi sai yau ta iya taci abinci.

Around 9 Hawwa na zaune kan gado tana duba wayanta tareda Ramla da yawanci ke tayata replying chats na yan wajen aikinsu dan kowa yaji tayi accident, Ammi nakan dadduma ta idar da salla but still tanakan dadduma tana jan charbi Baba yayi sallama yashigo dakin, da sauri dukansu suka dago kansu Baba yashigo yanama Hawwa murmushi yace "kinji sauki yarinyana?

Wannan dakuka natsu ahaka me kuke da waya?

Kinji sauki" Gyadamai kai tayi ahankali tace "eh Baba" kallon Ammi yayi dake shafe addu'a yace

"kin idar Zainab"? Gyadamai kai Ammi tayi takalli Ramla tace "tashi Ramla je dakin Umma zamuyi magana da Hawwa" hakanan dan faduwa gaban Hawwa yayi wannan dahar suna kada Ramla waje maganan me zasu mata? Wani ciwo gareta aka fada a asibiti? Daidai lokacin Aminu yashigo dakin dawata yar jaka kaman ghana masgo amman bottega ne mai bala'in kyau Baba yanunamai gabansa yace "zoka ijiye anan" ijiyewa yayi Baba yace "zaka iya tafiya Aminu" sannan yayi gyaran murya yadauki kujeran dressing mirror yazo wajen katifan dab da Hawwa itama Ammi tazo dab da Hawwa tazauna kan katifar, Baba yakalli Ammi data gyadamai kai yayi gyaran murya yaciro wayansa yabude yace

"Hawwa na aurar dake, ga sadakin ki nan" yanuna mata alert na wayanshi na 50M yace

"miliyan hamsin da dirhamin gwal dari gasunan" ya jjjiga mata jakan gabanshi, bugawa kirjinta yafara tana kallon Ammi takasa magana badai Baba yaji haushin Ni'ima yace ya aura ma Baban Yaseer itaba, Baba na kallonta yace "Ba Baban Yaseer bane mijinki ba Hawwa, na aurar dake ga someone even better, wanda ya fisa, yaro mai kunya, yaro mai natsuwa, ga dattaku ga girmama na gaba dashi, sunan mijinki Ibrahim Khaleel" bugawa kirjin Hawwa yayi sosai Ibrahim Khaleel Ibrahim Khaleel waye kuma Ibrahim Khaleel? Kaman Baba yaji abinda take tambaya anatse yace "Mahaifin Noor! Wanda ya ceto rayuwanki yakaiki asibitinsa sannan yabiya masu motocin dakika bata garin hatsari" Wani irin zabura Hawwa tayi ta yunkuro daga jikin pillow data jingina dashi a bango tana kallon Baba maganganun da Khaleel yamata na dawo mata see you soon! Babu wacce nakeso da bazan iya samu ba, bakinta har rawa rawa yake tace "Pops Dasauri Baba da Ammi suka kalleta basu gane metake cewa ba arude tace "Baba wannan mutumin daya kawo yarsa jiya da daddare asibiti? Ammi likitan daya kawomu gida? Shi wai kuke cewa kun auramin?" Dasauri duk sukace eh Baba yace "ai yagayamin kusan juna kece kika ceto Noor da aka sace" hannu Hawwa tadaura saman kirjinta dake bugawa kaman zai fito dasauri, Baba yace "Hawwa" cikeda fushi Hawwa tace "Baba kasan waye Khaleel kuwa?

Kunsan wakuka auramin? Eh Baba" shiru daga Baba har Ammi sukayi suna kallonta, zuciya ba dadi tace "Baba auri saki Khaleel yakeyi fa, dan shaye shaye ne Baba wih, dan giya ne Baba" tsayawa Ammi da

Baba sukayi suna kallonta ganin basuce komiba yasa dasauri ta matso kusada Ammi dake kallonta tace "Ammi wih dan shaye shaye ne babu abinda bayasha, banda haka ga auri saki ya maida mata kaman riguna yacire wannan yagaji yasaka sabuwa, Baba ni koshine namijin karshe aduniyan nan bazan aureshi ba na tsaneshi, bantaba haduwa da wanda na irinsa ba, ko kadan baimin ba, kucemai banyin auren, Baba bazan zauna dashi ba" kallon Ammi Baba yayi, Ammi ma takalli Baba hankali tashe Baba yace "Zainabu anya Hawwa ita kadaine?" Dasauri Hawwa tace "Baba nataba maka karya ne? Baba wih Khaleel dan giya ne ga auri saki ni bazan taba yarda da auren nan ba gaskiya cus shi ba mijin aure bane" sosai Ammi ke kallonta saikuma ta kalli Baba tace "Malam gobe muje wajen malamin dakamin magana muma Hawwa ruqiya" turus saikuma yakalli  Hawwa dake kallansu yace "Hawwa

bakiso kiyi aure ne kin fiso kiyita zaman gida kawayenki na cimiki mutunci akan mazajensu"?

Dafekai Hawwa tayi ganin Baba da Ammi basu fahimcetaba sun dauko magana daban, kaman zata fashe da kuka tace "Baba baku fahimce ni ba, bawai auren ne banaso ba, wanda kuka auramin ne ba mijin aure ba, Baba bakuyi bincike akanshi ba" da dan masifa Baba yace

"ke kinyi bincike akan shi ne?" Shiru Hawwa tayi saikuma ta girgiza kai alamun a'a, cikeda da dan masifa Baba yace "sau nawa duka duka kikaje gidansu aikin Noor da aka kiraku?" Ahankali tace

"sau biyu" dadan masifa Baba yace "mutumin da sau biyu kika hadu dashi shine zaki dingamai kazafi haka kinsan menene dan giya kuwa?" Yakalli Ammi yace "Zainabu tsakaninki da Allah zaki fadi badan ni ba bakuma dan Hawwa ba, kifadi iyakan gaskiyan ki har zuciya Khaleel yamiki kama da dan giya?" Anatse Ammi ta girgizakai tace "Hawwa ko kadan Ibrahim baiyi kama da dan giya ba, muna ganin yara masu shaye shaye munsani, tundaga kan halayyansu, mu'amalan su, yanayin magana da yanayin bakinsu ana ganewa Khaleel ba dan giya bane" dafe goshi Hawwa tayi ranta yayi masifan baci, Baba yace "kikace yana auri saki Ibrahima yasanar dani tun yana yaro dan shekara ashirin da hudu mahaifiyarshi kemai aure, duk yasaki matan ciki harda mahaifiyar Noor, baitaba neman aure da kanshi ba sai akanki daya ganki yaji kuma yanaso, sabida yayi auri saki ada baya nufin zaiyi dake ke zakiyi abinda za'a sakeki ne?

Ga mahaifiyarki anan zata koyardake yanda ake tattalin miji da sauransu"baki Hawwa tasaki idanunta na tsatso hawaye tana kallon Baba dake kare Khaleel kaman irin yayi shekara da shekaru dayasan shi shekaru dayasan shi yace "na natsu da natsuwar Ibrahima! Na yaba da hankalinsa da kyauta da sauransu, abinda na lura akan yaron shine yaro ne mai shagwaba wanda daga gani iyayensa sun sangartasa koda kin aureshi abarayin ne zaki iya samin matsala dashi sabida yasaba kome yakeso yana samu, wanda rayuwan nan babu wani bawa da baida aibu, inada nawa kinada naki mamanki nada nata bature yace nobody is perfect" Ammi tace "kwarai" Baba yakalleta sai kuma ya tausasa murya yace "Hawwa agabana aka cimiki mutunci aka zageki aka goranta miki sabida bakida aure kin zaci ina farin ciki da hakan?" Yayi shiru yanuna Ammi yace "an zageta, an zageni, an zagi tarbiyan damuka miki, aka goranta mini, aka kira diyata da tai kwantai, aka miki kazafi, kin dauka ina farinciki da hakan?" Jikin Hawwa sanyi yafara yi, anatse Baba yace "danabar dakin nan jiri ya debeni zan fadi Ibrahima yatareni" Baba yawani kalli saman dakin hawaye na gangaromai daga idanu kaman mai tuna abubuwa da dama yace "Ibrahima ya kamani, yarikeni ajikinsa kaman daman ya sanni daga wani waje, yakaini daki yabani kulawa da agaji na gaggawa, cikin tattausan lafazi yace Baba kadena damuwa zan auri Hawwa!" Sai kawai Baba yafashe da kuka sosai

yace "ko yaran cikina basu tabamin hallaccin da Ibrahima yayimini ba, ya fitar dani kunya, yanunamin soyyaya haka yanunama yata, yakawo iyayensa aka daura aure, wani awaje ya sharemin hawaye sai kene yanzu Ina sanar dake namiki aure zaki watsamin kasa a idanu" Baba yafashe da kuka sosai Ammi ta taso ganin da gaske Baba kuka yake tace "Malam dan Allah kayakuri abin baikai ga hakaba ya isa ya isa" Hawwa Baba yanuna yace "Zainab yarinyar nan tasan yanda nake sonta kuwa? Ita kadai nake gani natuna Aisha matata ita kadai, amman maisa Hawwa ke wahalar dani tana bani ciwon kai" wih at first Ammi tadauka Baba just lie lie cry yake but sosai Baba ke kuka, Hawwa tazo bakin gadon ahankali tadafa kafan Baba tace "Baba dan Allah kayakuri bahaka nake nufi ba dan Allah"Fashewa da kuka Baba yayi yace "Zainab kinsan shekara nawa rabona danai bacci? Wih tunda Hawwa takai shekara ashirin da biyar batai aure ba daga ranan har zuwa ana gobe zatai hatsari bantaba kwana gari yawaye ban tashi inyi salla inama yarinyar nan addu'a tayi aure tasami miji nagani ba, bana bacci bana iya runtsawa tunanin Hawwa nake, sai ranan da aka daura mata aure shekaran jiya shine nai bacci sai asuba natashi da jiya dakuma yau in 4yrs ina abu daya sai ranaku ukun nan na iya bacci sabida na aurar da ita" dasauri Ammi itama tace "Malam meyayi zafi haka? Dan Allah kayakuri ya isa" takalli Hawwa dake kukan bakin ciki ganin abinda Baba keyi sabida dan iskan Khaleel tace "Hawwa I know concerns naki, tunda ba kisan kai Ibrahim yake ba, ko saida yara, ko fashi, ke kaddarama yana shaye shayen ke ba matarsa bace? Ai mata Allah yabasu power da suna iya gyara mazajensu from bad to good, banda haka bayan Baba yazo damaganan na jera kwana biyu a asibiti ina alwala nayi raka'a biyu nayi du'aul istikhara wih naji na natsu da Khaleel and it's a sign auren ku zaiyi albarka, Hawwa koma meke damunki dake hanaki aure fight it this time, karki bari shedan yayi nasara akanki, auren nan yanda aka daura an daura kenan har abada kibar zancen rabawa" baki Hawwa tabude zatai magana Baba yadaga mata hannu.

EPISODE

7

•00

Cikin bacin rai Baba yace "idan kalma mara kyau zaki fadi akan Ibrahima na kiyi shiru kada ki fada don yana sosamin rai" shiru Hawwa tayi batasan me Khaleel yamusu ba especially Baba imagine ma harda Ammi, dukansu biyun basu yarda da itaba, just for peace Baba yadena kukan nan zata yarda tai shiru amman tai alkawari saita nunama su Baba waye Khaleel she will bring evidence and everything dan kome za'ayi ayi she will never ever accept yaron Pops din nan amatsayin mijinta ba!. "Hawwa kinji abinda muke fada miki?" Kallon Ammi tayi fuskanta ta share tass da bayan hannu ta kalli Baba tareda kakalo murmushin dole tace "naji shikenan na yarda babu komi" wani kayataccen murmushi Baba yayi yana share fuskanshi sai kawai ya rungumeta kaman zai cinyeta yace "nagode Hawwa, banso na tursasaki kiyi abu, nagode dakika yarda" sakinta yayi yace "cikin kudin sadakin nawa kike bukata nabaki inaso naba Ammin ki sauran asayo miki kome kikeso Ibrahim yace sati uku on 24th ne taron biki" wani abu Hawwa taji ya tsayamata awuya amman dai ta gyadamusu kai Baba yace "zamu fara shirin biki wannan gwal din kuma nida Aminu zamuje banki gobe mu boyemiki, yanzu gayamin nawa kikeso a kudin?" Ahankali tace

"banson komi Baba kuyi abinda yadace inada dan kudi ai ni" Baba yace "to shikenan zan dauki ko miliyan goma ne nasai miki filaye kisami kaddara sauran kudin ayi kayan aure dasu da gara" Ammi tace "zanje

Zaria jibi nadan shiryo nadawo saimu fara shirye shirye bakama hannun yaro afito da anko sabida kowa yasami dinki tunda lokaci ya kuro" Hawwa kawai tai shiru tana kallon Baba da Ammi dake planning sosai zuciyanta na kuna tana durama Khaleel ashar kirjinta na radadi kaman zata kama da wuta cus tasan auren is nothing but a game.

Har tai bacci tabarsu awajen planning bikinta

Ammi da Baba suke wih ko Baba ne amaryan sai haka. wuraren 3 na dare ta farka tareda taba wayanta tadan haska Ramla ne ke kusada ita tana bacci, sai Ammi a bakin gadon ta dayan edge din, kankame jikinta Hawwa tayi abin yataso mata what is wrong with her? She's on MP fa though tagama da asuban nan zatai wanka tafara salla, haushin kanta ta shiga ji sabida tunawa da yanda Ni ima use this feelings against her, iska ta fuzar ahankali ta zame ta sauka kasa sai kawai ta sulale ta kwanta akasan tiles din dakeda sanyi, kusan 20mins tana ahaka kafin yasoma lafawa bacci ya kwasheta anan wajen, cikin bacci taji ana kiran sunanta da sauri tabude ido Ammi ce ta kunna wutan dakin tace

"badai Ramla ta turoki kika fado kasa ba?"

Danne kunyan datakeji tayi tace "Ammi nakan fado kasa haka wani zubin" Ammi tace "ahh lallai sannu iyayen bacci mara kan gado, idan zaki wanka yanzu nasa ruwa a wuta bayau zaki fara salla ba?" Gyadama Ammi kai tayi ta tashi tana cire kaya Ammi tahau dadduma ta kabbarta salla wucewa tayi tafice Ammi tajuyo wih tunda ta farka Ammi ta farka sabida ijiyan zuciyan dataketa saukewa abinda yatasheta kenan, saikuma sauka datayi kasa aranta Ammi tace "kodai tama Baba magana ne ayl bikin next week akaita kawai".

Dawowa dakin tayi tazauna gaban madubi tana kallon kanta dayayi tsufa ahankali tace "anjima zanje saloon" tuna zancen Baba ya auramata

Khaleel sai kawai taji ranta yabaci kwafa tayi she has plan she will show Baba waye Khaleel she will get evidence, saita nunama yaron nan ita ba kalan sauran matan daya saba aure bane, she don't want him so bazata taba zaman auren nan ba, 3weeks is morethan enough for her to show Baba evidence kan waye Khaleel even if it means nemo all matan daya aura adah.

Wani simple riga da skirt tasaka tadauki dadduma ya shimfida itama tai salla suka idar ta gaida Ammi, Ammi tace "yajikin?" Ahankali tace

"Ipy lau" murmushi tamata "zanje zaria nataho damai gyaran jiki, dakin chan da akasa tarkace Baba yace yau duk zaisa afitar dasu a gyara tsaf anan za'a dinga tara abubuwan ki da za'a siyo mai gyaran ta sauka anan, saikuma inaso ki gayamin wani kalan kayan kitchen kikeso?"

Ita abinma dariya yadan bata sai kawai ta tashi tace "duk wanda kika saya Ammi, bari nai aikin office yau zani saloon gobe nakeso nakoma aiki" Ammi tabita da kallo tace "okay"

Wuraren 11 Baba yashigo yana kwalamata kira tana cikin shiryawa itada Ramla datace zata bita dasauri ta taho kofa, wani key mai kyau na benz yace "gashi mijinki ya aiko miki da motansa wai kidinga hawa naki har yanzu ba'a gama gyarawa ba tai condemn" key tadan harara kadan tace

"da keke zamu ai Baba ba nisa saloon din" sarai yasan halin yarsa watsamata mugun kallo yayi yace "mijinki ya bada umarmi ki hau tasa motar  wacce batama mijinta biyayya tarbiyan dana miki kenan? Wih zan cimiki mutunci fa" Kaman zata kurma ihu ta hadiye abu awuya tasa hannu ta amsa tace "yakuri" murmushi Baba yamata yace

"ko Kefa yar albarka yanada kyau mata tadinga bin umarnin miji tafi ganin haske arayuwanta" komawa ciki Hawwa tayi ta zauna turus akan gado ranta dukya baci Ammi tace "uwarfada tashi kuwuce kutafi kafin na sabamiki" mikewa tayi ahankali tadauki black veil na abaya dake jikinta dogo mai kyau ta daura aka tadauki wayanta da handbag Ramla ta fesa turare sannan suka fito, motar na kofar gida wata mahaukaciyan 2024 Benz ce grey, ga ledojin duk ajikin car seats din daga gani kasan sabuwa ce motar har kyalli take, Baba yace "kunfito wuce kutafi" sake hadiye abu tayi awuyanta tawuce Ramla tabita taje zata bude motan tasake tsayawa turus tadan kalli Baba ganin ita yake kallo yasa ahankali tabude motan ta shiga ahankali kaman bataso ta zauna Ramla ka tashigo tace "wowwww Ya Hawwa sabuwar mota ce kal wih Ya Ibrahim naji dake" mugun kallon da Hawwa tamata yasa taja bakinta tai gum, ganin taki tada motar yasa Baba yadaga murya yace "kuna jiran wani ne? Ko injin ya mutu ne azo aturaku"? Ahankali Hawwa ta tadamotan kaman bataso sannan taja motan ahankali sukabar anguwan motan dadi Ya Allah!

Wato better thing money kill am, steering wheel din kaman oil sabida yanda yake juyuwa ta dadi ba irin nataba da kaman tana dambe ba, wayanta ne yashiga ringing tahau kan hanya batare tadauka idanunta kan hanya takai wayan takai kunnenta batare data kallaba cikin murya mai dadi tace "hello" strictly taji muryanshi that 19:13

•00

sounds kaman yanzu yake farkawa daga bacci yace "da permission din waye kika fita?" Dawani irin sauri Hawwa tazare wayan daga kunnenta number ne kuma Truecaller ta bai fadamata waye ba kashe wayan tayi taidan tsaki ta ijiye Ramla ta kalleta ringing wayan yashiga yi taki kallon wayan ma Ramla tace "Ya Hawwa ana kiranki" ahankali tace "share" har sukakai saloon din kiranta yake, kashema wayan tayi daga baya gabaki daya suka shiga saloon din batason tai kitso kar kanta yayi ciwo kawai tsifa da wanke kan da blow drying shiko aka mata cikin 1hour aka gama tabiya kudi suka fito Khaleel tagani zaune kan bonnet na motanta yadaura kafa daya kan daya dagashi sai short na rick owens nude more like milk, da armani polo mai kyau maroon ga pcap akanshi milk shima dayamai kyau crocs ne akafanshi duk wanda zaiga Khaleel saiya juyo yakara kallonshi cus baimayi kama da Nigerians ba kaman irin black black American people din nan ma har yanda yake dressing, Ramla ta washe baki ganinshi tama wuce Ya Hawwa ta taho wajenshi da gudu tace "Ya Ibrahim ina yini kazo" murmushi kadan yamata yace "Hi Ramla kema kinyi saloon da wanchan yarinyar nan ne"?

Yanuna Hawwa dake tahowa sarai tajishi takuma shaka but ta daure sabida Ramla, akunyace Ramla tace "ni yau kwanan kitsona uku saisa banyiba, Ya Hawwa na rako kawai" zuwa wajen Hawwa tayi azuciye zata wucesu tabude mota karaf taji an rike mata hannu kafin tai magana kawai Khaleel ya fizgota jikinshi da shegen zafin nama, kafin tasake magana taji hannunshi cikin nata ya karbe key motan ya wurgama Salman ya chabe yace "take Ramla shopping then home Salam, I want to talk to my wife privately!" Kawai ya kankame Hawwa

ne turata baya kunya kawai yarufe Hawwa na masifa, ga Ramla data saki ido baki hanci tana kallon abinda Khaleel kemata, ga jama'a, ga su securities dinshi, she had no choice haka ya dinga turuwanmai har jikin motanshi yakaita yabude

kofa yamata rumfa agabanta kaman zaiyi hugging nata yakalleta yace "get in" zatai magana yace "i will kiss and touch you all over kikamin gardama!" Runtse idanu Hawwa tayi ta tabbatar Ramla taji maganan wih harsu Salman da kowama, kaman zata shige kasa, da kyar tabude idanunta Ramla tadan kalla dahar ta shige gaba abinta tana mata bye tana washe baki na murna da farinciki, da sauri kawai ta juya ta shige without saying a word, shima yashige yana rufo kofan motan yace "let's go" Aharzuke Hawwa ta kalleshi tace "wai is something wrong with you? How dare you touch me like that a public?" Hannu yasa yazare pcap na kanshi yakalleta babu wasa kan fuskanshi yace "duk randa kika kara fita without kin sanar dani sai ranki yabaci I forgive this one but next one l won't" tsayawa Hawwa tayi tana kallon ikon Allah abinma sai yasa tai dariyan takaici tace

"ikon Rabbi! Auren da Baba yamin dakaine yasa kake wani takama kana feeling kaman u own me?" Kallonta Khaleel yayi baice komiba hakan yasake pushing Hawwa to the wall, tace "guess wat nariga nama kaina alkawari before this 3weeks I will expose who you are to my family! I trust Baba da kanshi zai raba auren nan daya mana l will prove to them cewa you are nothing but a womanizer sai aure aure kaman ayu ga shaye shaye da party BfF din dujal, I'm Hawwa! I can never settle for less! I want a man dayaci sunanshi man not yaro! I want a responsible man not Pops hayl want a man that shoulder responsibilities not wanda ake shouldering responsibility shi! Ni da kai are two world apart trust me you need plenty years to get to world din danake, so forget kayi abin nan waishi daurin aure but Hawwa can never ever be yours" wani juya idanu Khaleel yamata kaman zaiyi bacci yayi shiru chan yace "feel free! Do whatever you want! Khaleel yariga ya sameki! Dudda kina chan world dinki but without stress na mika hannu na ciroki daga world din nakawoki my own world dakika tsana so much Kululuwa, matar dujal bff" dasauri tawani yunkuro kaman zata dakeshi tace

"nace kadaina kirana sunannan!" Murmushi kadan yamata yace "to Yar Sanda!" Wani irin runtse idanu tayi kaman zata dakeshi cus he's pushing her yayi murmushi kadan baice mata komi ba, afadace tace "ina zaka kaini? Ba hanyan gidanmu bane nan ba?" Dan kanshi ya sosa yana kallonta kaman yanda take kallonshi murya chan ciki yace "we are going to hotel!" Mummunan gaban Hawwa yayi.

[9/28, 8:18 AM] +234 806 486 0007: YA ALLAH ZAN FARA THIS UPDATE DA ADDU’A! YA ALLAH KAGA YANDA NABADA FREE PAGES NA SAUKE HAKKI, YA ALLAH DUK WANDA YACI HAKKINA YA KARANTAMIN DAIDAI DA HARAFI DAYA A LABARIN NAN YA ALLAH BAN YAFEMAI BAN YAFEMATA BA! HAR ABADA! ALLAH KABIMIN HAKKI NA! YA ALLAH KA SAKAMIN!!

WAYANDA SUKAI SUBSCRIBING THANK YOU! BUT IDAN KUN FITAR KUMA ALLAH YA SAKAMIN BAN YAFEBA!!

HELP ME GROW APPLICATION NAKESO NAYI JARI NAKE TARAWA🥲

EPISODE 4️⃣1️⃣

Wuraren 5 Hawwa ke bude idanunta tana kallon saman dakin komi daya faru nadawo mata, hawaye masu dumi ne sakko daga idanunta, ahankali tafara mosti da idanun dake mata nauyi sosai tana juyowa kanta yayi sauki kaman ba nata ba yanzu tana iya juyawa yadena banging, Ammi ta gani a tsakar dakin kan dadduma ga charbi a hannunta tanaja maida idanunta tayi tarufe she can't look at Ammi, knocking kofan akayi da sauri Ammi ta tashi tace "shigo" tadaga dadduma tana linkewa daidai Dr yashigo tareda Nurses yazo gaban gadon yana kallon Hawwa data lumshe idanu Ammi tace "Dr har yanzu bata tashi ba nadamu abinci fa"? Murmushi yama Ammi yana duba BP Hawwa dayasan ta tashi yace "maganin hawan jini nasa bacci amman karki damu zata tashi saitai wanka" ijiyan zuciya ya sauke yace "Alhamdulillah BP yasoma sauka" anatse yace "Miss Hawwa open your eyes" ahankali Hawwa tashiga bude idanunta tadan kalli Doctor kadan saikuma ta sauke idanun kasa kawai nauyin kowa takeji, Dr yace "ya ciwon kan? Akwai wani abu dayake miki ciwo yanzu?" Girgizamai kai tayi murya kasa kasa dabaya fita da kyau tace "no" Dr yace "okay that's great" yakalli Ammi yace "Mama help her to change tadan gyara za'azo a gyara gadon akawo mata abinci kuma, an mata booking massage Yallabai yace bayanta na ciwo, masseuse zasu mata massage din, zatasa hospital clothes bama barin patient namu nasa kayan gida" gyadamai kai Ammi tayi tace "to" Nurses suka ciremata drip din suka fice Ammi taje gaban gadon tana kallon Hawwa da idanunta ke kasa ta kauda kanta gefe dasauri jin Ammi tazo wajen, Ammi dake kallonta tace "Jidda na ya jikin? Babu abinda ke miki ciwo kuma"? Gyadama Ammi kai tayi ahankali batare data kalleta ba tace "eh" cikeda so Ammi tace "tashi muje to kiyi wanka ki chanza" Ammi takai hannunta tadagota tasowa tayi da karfin hali ta sauka daga gadon Ammi tariketa har bayi tabata gadon Ammi tahada mata ruwan wanka, tadawo dakin tabude jakan kaya da Baba da Ramla suka kawo musu jiya taciro brush da zani, saikuma pad datasa Ramla tasa ajakan tadauki daya da wando takoma bayin ta ijiye mata tasake fitowa ta yaye zanin gadon daidai nurse tashigo da wani ta shimfida mata da hospital gown mai kyau na yan gayu sannan tafice saikuma masu abinci suka kawo mata fruits da oat, dasu chips da egg da salad da sausage ga bread saikuma maganin dazata sha a gefe cikin wani glass covered container Ammi sai kallo take komi na masu kudi daban ne.

Kusan 15min tayi abayin Ammi takoma wajen bayin tace "kin gama Hawwa"? Ahankali tace "eh" Ammi tabude tashiga tana kallon yanda taki yadda su hada idanu, maidata gadon tayi tana kallon yanda white and blue flowers hospital gown din yamata kyau ta zaunar da ita tana daga tray na abincin tana ijiye mata tace "yi maza ci kafin sudawo" yatsine fuska tayi batada apatite ko kadan kauda kanta tayi asanyaye tace "Ammi bazan iya ci ba" sosai Ammi ke kallonta saikuma ta matso ta zauna abakin gadon anatse tace "Hawwa" asanyaye Hawwa tace "Naam" batare data kalli Ammi ba, lumshe idanu Ammi tayi tabudesu

tace “look at me Hawwa” girgizama Ammi kai tayi dasauri lips nata suka shiga rawa tace “Ammi bazan iya ba” wani iri Ammi taji, hannunta tasa tadauke tray na abincin ta ijiye akan table na dakin sannan ta matso dab da Hawwa ahankali tace “Hawwa look at me” daidai lokacin hawaye yasauko daga idanunta tace “Ammi bazan iya kallonki ba, Ammi banmasan ta yaya zan kalli keda Baba ba” sai takai hannayenta biyu tadaura kan fuskanta tafashe da kuka mai tsuma zuciya she’s hurt, Ni’ima hurt her beyond duk yanda zatayi bayanin tace “wlh, wlh, wlh  Ammi ni ba yar iska bace bantaba amfani da kaina ba, Ammi that’s not me, bazan tabama wani fyade ba” hawaye Ammi tashare daga fuskanta Hawwa tabata tausayi sannan takai hannunta takama hannun Hawwa tasauke takai hannunta tajuyo da habanta fuskan Hawwa yajuyo Ammi tanuna kanta tace “Hawwa ni mahaifiyarki ce kina gani aduniyan nan akwai wanda yasan yarsa sama da mahaifiyar ta? I know you Hawwa, nasan tarbiyan da muka miki, I know who you are? Dagani har Babanki babu wanda yama dauki maganar da Ni’ima tayi da mahimmanci, Hawwa yau koda haka kike ko kinfi hakama muna sonki and we will always love you, Hawwa ke y’ata ce inasonki aduk yanda kike aduk yanda kika zama, kinji yarinyana, ki manta da duk wani abu data fada, come here” dasauri ta rungume Ammi tana sake samin wani karfin guiwa iyaye daban suke idan suka nuna they’re with you and they stand with you kafi jinka very strong kankame Ammi tayi tana kuka harwani rera kukan take kaman marainiya tace “Ammi menama Ni’ima? Why all this hate? Sabida ni Ni’ima tazageku ta ma Baba rashin kunya, Ni’ima tamin gori tama Baba gori, Ammi me namata eh”? Tawani ja numfashi tana rera kuka tace “bazan taba auren mijinta ba, Ammi sabida bansami miji ba banda aure shikenan na zama dustbin? Kowa yadauko shiritanshi akaina? Ammi inaso nai aure nahuta maybe only then Ni’ima zata yarda dani I’m not after Baban Yaseer, Ammi babu abinda kemin dadi“ cikin dan fushi kadan Ammi tace “zaki kashe kanki akan Ni’ima ne? Hawwa that girl obviously doesn’t deserve you, abu dayane bazanyi supporting naki ba shine kisamakanki damuwan Ni’ima, Hawwa don’t kill yourself akanta, Ni’ima don’t deserve you Allah use this chance ya nunamiki waye ita, so is time kifita daga rayuwansu both ita da mijinta and move on, toxic people ne dukansu biyun, kiji sauki kidena tunanin komi, I didn’t train you to be weak or to be crying for any girl, Hawwa you are a strong girl wacce guguwan iskan mountain baiyi putting baki down ba saida kikai destination naki, shit happens in this life, friends comes and goes, relationship ends that doesn’t mean bazamu cigaba da rayuwa ba, close chapter Ni’ima and move on learn from your mistakes, no more room for wacce wishes you death, your secrets should be for your stomach idan ba ni ko mahaifin ki ba babu wanda ya isa yaji sirrin ki, move on and be a better person kinji, kihakura da Ni’ima, tace taja miki layi kema kijamata layin kinjini” gyadama Ammi kai tayi ahankali tana kuka har lokacin, Ammi ta matso ta manna mata kiss a goshi sannan tadauki tray na abinci cikin masifa tace “nayi tir da dabi’un Ni’ima ayahya taje zata gani indai duniya ne fadi gareta, Allah zai saka miki” tashiga bata oats tana sha, masu massage sukazo akama bayanta massage dataji kaman an mikar da ita an ciremata duk wani bending da ciwon jiki, no wonder massage keda tsada ashe haka akeji, duk wani tsamin jiki saida suka fitar bacci yayi awon gaba da ita haka nurse’s sukazo suka kara mata fixing drip din tana bacci mai nauyi.

Tun asuba Allah sanya alkhairi akema Baba, kafinma yasamu yabar masallacin was around 8:20 sai farin ciki yake nanma wasu suka sake tsareshi anan waje anamai Allah sanya alheri wani kara son Baba ma

akayi a unguwan Baba tsabagen murmushi kumatunsa har ciwo yake sai wajajen 9 yawuce gidansa da sallama ya shiga cikin gidan Maman Ni'ima daya gani a tsakar gidan kan kujera yasa yaci tura ya tsaya, Mama ta washe baki tace "ahhh Malam ka shigo barkanmu da safiya ai tundazu nazo nake jiranka" dan jim Baba yayi saikuma yakaraso ciki yace "Malama Maimuna ya kwana biyu ya yara ince dai kinaji daga garesu"? Murmushi Mama tayi tace "kowa na nan lpy, satin daya gabata ma Usaina ta haihu an samu Abdulwahabu" anatse Baba yace "Masha Allah, Allah ya raya" ya kwalama Ramla kira data fito daga dakin Hawwa tace "gani Baba" Mama yanuna mata yace "kaita ciki bari na zaga nazo" Mama ta mike tabi Ramla ciki tanabin dakin Hawwa dakenan tsaftsaf da kallo shikuma Baba yawuce makewaya.

takama hannun Hawwa tarike gam cikin wani irin murya mai rauni tace “Hawww…….waaaaa!” Kawai hawaye Hawwa taji sunzo idanunta tadai daure tahanasu zubowa takalli Ni’ima data rike mata hannu tace “yanzu kuma mena miki Ni’ima kikazo nemana?” Daidai lokacin Baba na bugo sallama yana shigowa tareda Aminu suna hira ganin Ni’ima tarike hannun Hawwa yasa ya kirne fuska suka kame awajen, cikin sanyin murya dake nuna nadama Ni’ima tace “Hawwa banda words to justify whatever I did to you and your family, Hawwa bansan meya shigeni ba, I couldn’t believe nine ke yunkuri inacewa zan kasheki da gaske kaman aka banni zan iy…..iya….” Muryanta yashiga rawa takalli Ammi dake kallonta ta kofa tajuya takalli Baba tace “nama magabatana kuma iyayena maganganu marasa dadi I’ve lost everything, Hawwa Baban Yaseer yasakeni tun ranan hospital din nan ina gidanmu har yau” ahankali Hawwa ta kalleta tausayinta na ratsata da rashin jin dadin news din, gyadama Hawwa kai tayi Ni’ima tayi ganin taga tausayinta akan idanunta yasa cikin sanyin murya tana kuka tace “ya kwashe yaranmu bansan ina yakaisu ba nakira school ance basa zuwa” tafashe da kukan damu da rashin gata Hawwa taji zuciyanta ya tsinke awani irin hankali Ni’ima tace “yau an koreni daga wajen aiki Leadway sun tura video abinda namiki to NMCN anyi revoking license dina! My hospital fires me” Runtse idanu Hawwa tayi she knows what nursing means to Ni’ima, shine kadai profession datake so aduniya, cikin muryan kuka Ni’ima tace “idan bakiso nakashe kaina Hawwa ki yafemin ki manta da abinda namiki komi yawuce I’m sorry, I’m really very sorry” tafashe da kuka sosai zatai kneeling da sauri Hawwa takai hannunta ta tareta kaman abinda Ni’ima ke jira kenan ta shige jikin Hawwa ta rungumeta  ta kankameta tana kuka Hawwa ta tsaya turus paper bag dake hannunta yafice yafadi akasa idanunta suka cicciko da hawaye dago idanunta tayi tahada idanu da Ammi data mata mugun kallo kawai tasaki labule takoma cikin daki abinta, Baba ma yakada kai yajuya rai abace kawai yayi zaure Aminu yabishi, kaman jira Hawwa take tasaka hannayenta abayan Ni’ima ta hugging nata back murya chan kasa tace “it’s okay stop crying ya isa, kinsan anytime kikai kuka haka yana saki ciwon kai” girgiza kai Ni’ima tayi ajikin Hawwa tace “Hawwa I’ve been a bad friend I’ve hurt you the most, I can’t forgive myself harsaikin yafemin dan Allah, Hawwa ban cancanci yafiya ba” cikeda tausayinta Hawwa tace “nayafe miki Ni’ima please stop crying now” tadagota daga jikinta tashiga sharemata hawaye tace “dan Allah kidena kuka yawuce”

Gyadamata kai tayi, Hawwa tace “gobe zanje office I will see what I can do about license naki Ogana has good connection he can help, I know what nursing means to you bazan bari kiyi loosing nashi ba okay” Gyadamata kai Ni’ima tayi, murya chan kasa Ni’ima tace “zaki tayani kiran Baban Yaseer kibashi hakuri ya maidani gidana? Banda ko sisi banda aiki yanzu I need him please kitayani kiransa” abu Hawwa taji ya tsaya mata a wuya takasa motsi takasa cemata eh ko a’a, Ni’ima tace “please feel free ni da ke are one kinji Best” hannunta Hawwa ta kalla saikuma tadauki paper bag din tana dubaw,a Ni’ima na kallon jakan Hawwa tashiga ciro abubuwan ciki tana neman wayanta, wasu expensive designers perfumes ne sai box na polo diamond watch da another box na LV brackets sai kuma cute note, ganin bataga wayanta ba yasa tace “Innalillahi na manta ban karbi wayana daga hannunsa ba” abu Ni’ima ta danne dataji ya tsayamata a kirji tace “wane?” Yatsine fuska Hawwa tayi kadan tace “Khaleel” murmushin dole Ni’ima tayi tace “ohh wai mijinki, shiya baki gifts haka”? Gyadamata kai Hawwa tayi not paying attention to her sabida yanda taji ranta yabaci yagama tabata yatafi da wayanta, hannu Ni’ima tasa tadauki note din ita adole sun dawo kaman da tace “read note daya miki mana bari na karanta miki” tai murmushi tace “yarubuta my first gift with love to Mrs Lee Kulu Yar Sanda” dan tsaki Hawwa taja tace “dan rainin wayau” Ni’ima tace “he’s so romantic gurl common ina kukaje”? “Hawwa!” Ammi ta kwalamata kira dayasa Ni’ima ta tashi dasauri

tace “bari natafi har yanzu Ammi fushi take dani gobe zanzo maybe by then yakawo miki wayan sai mu kirashi”gyadamata kai Hawwa tayi ahankali tace “take care” Ni’ima tace “I love you Best” baki Hawwa tabude zatace love you too kaman yanda sukeyi da saita kasa furtawa murmushi tamata ahankali mai taushi tace “thank you agaida Mama” juyawa Ni’ima tayi tayi zaure tana tafiya ahankali hoping Hawwa zata kirata ko agogon nan ne tabata amman taji shiru tace shikenan Hawwa ta chanza ba haka Hawwa takeba da ba, ko waya Hawa tasaya zata iya sadaukar mata amman yau ko kudin ma datace batada su Hawwa bata bataba, ga gifts tagani but Hawwa couldn’t give her a thing.

Komi Hawwa ta kwasa ta shiga daki da sallama Ammi ta kalli Ramla tace “fita zanyi magana da Yayarki” fita Ramla tayi ganin yanda ran Ammi yabaci tana fita Hawwa tayi wajen Ammi dasauri tace “Ammi dan Allah kiyakuri yazanyi I have to talk to her amman naji maganan ki bazan maida ita kawata kaman d’a ba!” Kabar da hannunta Ammi tayi daga jikinta cikin tsananin fushi tace “you are very very very stupid Hawwa!”Dasauri Hawwa ta kalli Ammi dan bata taba zaginta ba, rai abace Ammi tanuna kanta tace “is something wrong with your brain? I expected you kice kinji kin yafe let’s end things kaman yanda ita tai initiating at first ki sallameta but kin tsaya kina hugging Ni’ima are you mad?” Baki Hawwa tabude tace “Ammi wlh bah……” “yimin shiru!” Ammi tafadi tana mata ihu, Hawwa tayi shiru tasauke kanta kasa Ammi tace “imagine kun fita keda mijinki yabaki gifts wannan kawar kike nunamawa har tana tayaki karanta note din da mijinki yarubata miki, you are telling her zaki ma Oganki magana kan licence dinta, zaki tayata kiran Baban Yaseer what is your business with Ni’ima and her affairs sai Ni’ima ta kasheki zakisan ta tsaneki ba kawar arziki bace?”

Ammi tai ihu she don’t care at this point uban kowa yaji Baba yashigo dakin yace “da kyau Zainabu wanke miki ita tunda kunnen kashi gareta” Ammi tace “Uwarki ce Ni’ima ko ubanki da bazaki iya hakura da ita ba can’t you leave with out her? Wlh kika kira Baban Yaseer kokikai magana kan licence dinta sainayi mummunan saba miki, Hawwa kika kara jawo Ni’ima jikinki wlh saina zame hannuna a lamarunku tunda ke kinsaka differentiating good people from bad, you’re a criminologist but kin kasa karantan Ni’ima kisan criminal ce ita all she’s doing dake is friends with benefit bata taba sonki ba, yau tazo wajenki sabida tasan u might be able to get her licence back for her, tasan mijinta na sonki kina karansa kika cemai yadawo da Ita zai dawo da ita, this gurl has been benefiting from you right from day one, Ni’ima tafi kowa cin albashinki saitaci tarage sauran mu yan uwanki kike rabamana” Ammi bambami takema Hawwa bana wasaba, tace “yanda kike kashema yaranta kudi kanninki da yaran kanninki basu samu haka daga jikinki suci, duka abinda kika mata arayuwa bai hana rana daya ta kwance miki zani a kasuwa ba ta zagi ubanki ta zagi uwarki ta goranta miki yanzu shine still kike neman goyata abaya kiyi Allah baki sa’a nina tafi zaria nafasa kwana gidan nan, Ramla zoki hada kayanmu mutafi”

Dasauri Hawwa tarike kafanta tana girgiza kai tace “Ammi dan Allah kiyakuri” Baba shima yace “Zainab yakuri yamma tayi bani barinki kishiga hanya yanzu” kaman Ammi zatai kuka tace “Malam Hawwa na batamin rai, tana bakantamin rai, haba haba dan Allah gamai sonta ta tsaya tana gayamana mashayi ne menene menene, ga mara sonta takasa ganewa binta take ido rufe kaman makauniya,ana nuna mata

gaskiya tana kulle idanu ina dalili kasheni takeso tayi da bacin rai da takaici nagayamaka bazan kwana ba Malam" Baba shima cikin masifa yace "shikenan kin batama mahaifiyar ki wacce ita kadaice bata fushi dake aduniya rai, matarnan ni da ita bama hammata iska muke akanki sabida yanda bataso ina fada akanki ina damunki, jibi yanda kika bakanta mata rai yau Hawwa kinji dadi ko"? Tashi Hawwa tayi sai kawai ta rungume Ammi tafashe da kuka tace "Ammi dan Allah kiyakuri trust me I don't consider Ni'ima my friend anymore and namiki alkawari bazan kara bari tasan sirri na ba kawai tabani tausayi ne somehow I feel responsible for her situation and condition da Baban Yaseer baiyi all abubuwan nan ba da yanzu suna tare abinsu but bazan karaba kiyakuri Ammi na forgive me dan Allah" shiru Ammi tayi saikuma ahankali tace "naji nahakura ya isa, kawai abin namin zafi arai ne yanda kike yunkurin dawo da makashinki rayuwanka" Baba yace "Allah ya kyauta ai ta kuskura tai haka saitaga bacin raina" ahankali Hawwa tace "bazanyiba Baba" wucewa Baba yayi yafita Hawwa takai Ammi gado ta zauna sai kawai ta kara rungume Ammi, ahankali Ammi tanuna mata wasu shopping bags tace "kinga abinda Ramla tayi taga opportunity" dan murmushi tayi kadan tace "yarinya ce Ammi" ahankali Ammi tace "ina kukaje?" "Wani shagon dinki aka aunani hmm" ta tabe baki Ammi tai murmushi tace "muga abubuwan".

[10/6, 10:39 AM] +234 706 565 5343: EPISODE 51

She wants to be Hawwarh's best friend, wannan abubuwan da ada zatai sharing da Ni'ima gwara tayi da ita, tabata labaran hakan zaisa ta manta da Ni'ima, Ammi ta karba tana budewa tarike baki tace "au dan gidansu yartawa yake cewa Yar Sanda Kulu lallai Ibrahim yacika sarkin tsokana" Ammi tabude kwalin agogon taciro tana kama hannun Hawwa ta dauramata tace "masha Allah cip cip idan gobe yazo saikisa yaganki dashi yaji dadi haka akeyi ma miji" Hawwa tadan turo baki tana tauna baki batadai magana ba gudun karta batawa Ammi rai Ammi tasamata bracelet din shima yamata kyau sannan ta bude turarukan ta feffesa mata itama Ammi ta fesa anata jikin tace "uhm ni Maman Amarya nima nayi kamshi" dan murmushi kadan tayi Ammi tace "kai gaskiya mijinki ya san kan turare Hawwa kinji kamshi" dasauri tace "Ammi nabaki ki daukesu ni dama inada turare na" dakuwa Ammi tamata tace "kwal ubaki Hawwa mijin naki yamiki kyauta zakimin, kaji yarinya inga kin bama wani saikin sani" turo baki tayi ta tashi kawai tana rage kayan jikinta Aminu yayi sallama yashigo wani waya daban yakawoma Hawwa yace "Ya Ibrahim yace nakawo miki" wayan takalla Iphone ne bamatasan wanne ba ganin Ammi na kallonta ta wutsiyan ido yasa tasa hannu ta karba tace "to" ta ijiye tawuce bayi.

Around 10 duk sun kwanta ita Hawwa sabida zatai azumi gobe Ammi kuma sabida zatai tafiya gobe, sabon wayan dataki bi takanshi tuntuni ne yahau ringing ita batamasan sim dinta ne ciki ko wani dabanba hakanan dai taji bazata dauka ba, wayan na karewa yashiga ringing again Ammi tace "wai ba ke ake kira ba Hawwa nafasan ba bacci kikeba" tashi tayi ta sauka daga gadon tasa hannu tadauki wayan akan mirror tadawo gadon ta kwanta sannan ta danna wayan takai kunnenta sabida Ammi yasa ta kwantar da murya sosai hakan yasa muryanta yayi wani irin dadi ahankali tace "hello" lumshe idanu Khaleel yayi yana gyara kwanci afalo ashagwabe yace "I'm hungry Kulu" wani iri Hawwa taji yanda yayi magana hakan yasa tayi

shiru, Khaleel ahankali tace “I don’t feel like eating abinda chef namu suka dafa, nazo kimin girki Kulu?” Runtse idanu Hawwa tayi tace “nace banson sunan nan” ahankali yace “but Hawwah is Hawwa Kulu” Shiru Hawwa tayi the way yake kiran Hawwa dadi, sabida Ammi tadaure tace “bacci zanyi zan tashi nayi azumi anjima good night” zata cire wayan daga kunnenta yace “but it’s not Ramadan, azumin me kikeyi ramuwa?” Shiru tayi ta lumshe idanu kaman bazata amsashi ba tace “nafila ina azumi Monday and Thursdays” cikin yar karaman murya yace “nima zanyi” yayi shiru jin batace komiba Khaleel yace “sainai addu’a Allah karya baki ikon bata auren mu, I want to live my life with you” yafadi ahankali baimasan mesa yake fadin hakaba but kawai yanaji ajikinshi bazai iya rabuwa da ita ba dan juyawa Hawwa tayi ganin Ammi tayi bacci ga ijiyan zuciyanta tanaji hakama Ramla yasa ahankali tace “you’re a liar! Kaida ke wulakanta mata bakasan darajansu ba, imagine locking your Baby Mama in jail, Allah bantabaji I hate someone kaman the way na tsaneka ba” shiru Khaleel yayi sai kuma chan yace “do you love my gift?” Cikeda tsana tace “I will never love anything that comes from you” shiru yayi baice komiba Hawwa kawai tazare wayan daga kunnenta daidai yasake kira kaman bazata daukaba tadauka kafin yayi magana tace “how could you send that video to Nursing Council don’t even deny it nasan aikinka ne, why would you do that to my friend?” Hamma taji yayi yace “zan fita I know you don’t have friends so bansan wat you are saying ba bye” Hawwa tace “aikin kenan party giya da mata” murmushi yayi yace “gashi na aureki” zatai magana ya katse wayan jitayi ranta yana kuna yana susa tasan yanzu club zaije maybe Allah kadai yasan time dazai dawo shiru tayi sai chan ta tuna yanda yamata kiss a kumatu a mota dasuri takai hannu tashiga share kumatunta  kaman yasamata dafi ahaka tai bacci.

Washegari around 8 suka fito dudda tanajin bakin cikin shiga motan nan haka ta shiga Ammi tafara kaiwa park sannan tawuce office.

Tundaga gate ake mata yajiki ana mata Allah kyauta tana zuwa direct office na DIG tayi tai knocking yabata izinin shigowa yana ganinta yadakatar da rubutun dayake yace “Hawwa are you sure you’re strong enough kidawo aiki?” Murmushi tamai tace “yes Sir thank you” anatse yace “welcome back” gyadamai kai tayi ganin ta tsaya bata wuce ba yasa yace “akwai wani abu ne?”

Gyadamai kai Hawwa tayi cikeda damuwa, seat dake gabanshi ya nuna mata hakan yasa ta zauna akan kujeran ya ijiye pen na hannunshi yace “I’m listening Miss Hawwa” gyadamai kai tayi anatse tace “Sir I have a very serious problem I need your help” gyara zama DIG yayi dan yana bama Hawwa respect da girma dan ijiyan zuciya ta sauke tace “Sir I’ve never been to Senate President house banda time din nan damukaje aiki, I know nothing about them or household nasu” with so much anticipation DIG yace “what’s with Excellency Hawwa?” Ijiyan zuciya ta sauke cikin raunin murya sosai tace “Sir ranan danai

accident ina hospital Babana yabasu aurena, sai  bayan mun dawo gida anyi discharging dina ake sanardani wai wannan yaron nasa Khaleel aka auramin" tayi maganan hawaye mai zafi na sauko mata DIG kanshi was in shock yazaro idanu yana kallon Hawwa yace "you mean Khaleel Baban Noor"? Gyadama DIG kai tayi bakinta na rawa tace "I have no idea me suka gayama Babana, banso Khaleel yake yakarani acikin sahun matansa sabida yayi using dina and dump me bayan 1 or two weeks" Ko kadan DIG baiji dadin news dinba but still cikeda damuwa yace "Hawwa akanme mahaifinki zai bada auren ki batare dayayi bincike ba? I'm not saying that because maybe zasu miki mugunta or something no su basa wannan, kawai dansu baisan menene aure ba, baisan darajan auren ba, mata are like papers zai iya bude this page ya yaga and open another page, so why will your father get your married to such kind of man"? Bayan hannu Hawwa tasa tagoge idanunta tace "sabida he's tired of me, yagaji da yanda nake zaman mai agida ba miji" DIG ko kadan baiji dadi ba yasakeyin shiru sai chan yace "to wani help kike magana zan miki"? Share fuskanta tayi tass kaman batai kuka ba takalleshi tace "I want you to come with me Sir muje ka gayama Babana the type of Man Khaleel is cus wai on 23RD this month za'ayi biki zan tare, I don't want this marriage I don't want to be victim of circumstance na gayama Babana all I know yaki yarda I'm sure ka tayani gayamai zai yarda".

[10/6, 10:39 AM] +234 706 565 5343: EPISODE 52

Kallonta DIG ya tsaya yana yi kaman mai lissafi na kusan 2min sai chan ya sauke ijiyan zuciya yace "Hawwa listen ki fahimceni keba yarinya bace I will be very raw in whatever I will tell you now" yadan sauke ijiyan zuciya yace "I'm a father inada yara mata babu wanda ya isa yazo yace zai aure yarana nabashi batare danayi bincike ba, for mutanen nan suzo mahaifinki yadauke ki sharp sharp batare daya damu dako kinaso ko bakiso, ko kinsan guy din ko baki sansa ba yabada ke only mean one thing" yadanyi shiru yana kallon Hawwa yace "just like rest of the victims parents kema maybe mahaifinki just did it for money ne so kina gani koda zanzo nace gashi gashi mahaifinki zai yarda akashe auren?" Hawwa tai shiru yace "saikuma second abu, Hawwa you've been in this job kinsan yanda aikin gwamnati yake, Baban yaron nan sune Nigeria gabaki daya do you want me to be on the bad side of such kind of people?? Naje nace kaza kaza ko baban ki baice ni ba ne las las zasu gano nine kinsan abubuwan da hakan can cost me?"

Yasake shiru yace "banda haka this is personal matter not work related, maganan aure ake ni as Oganki ko Boss dinki baikamata na shiga ba sai inzo naji kunya nan gaba cus of What If dayawa dana hararo in the case, what if ke bai sakeki like the rest of the matan ba? What if ya zauna dake har abada? Hawwa you have power what if you somehow influence him ya gyara all those hali and changed? Idan ya chanza is a good thing since he's not a murderer ko wani kidnapper" Ahankali DIG yace "just think it through but I don't think is proper for me to interfere Hawwa, kiyakuri but I don't think hurumina ne tunda har Babanki ne yabada ke da kanshi just pray and seek Allah guidance Allah sadaki da alkhairinsa" hawaye Hawwa taji ya zubomata sharrrr tai shiru a office din anatse DIG yace "so sorry Hawwa" tadade ahaka

sannan ta share fuskanta  tamike tace “is it okay nai resuming gobe Sir I have to be somewhere”? Gyadamata kai yayi yace “sure take your time” wucewa tayi tafita yabita da kallo tawuce tashiga motanta ta tada Maman Noor kawai tafado mata arai, she’s her only second hope.

Sanin tana prison hakan yasa tawuce prison na mata, parking tayi tana zuwa ta nuna ID card nata tawuce office na prison warden din ta zauna bayan sun gaisa da Matar Mrs Adebayo tace “wakikeson gani yau Miss Hawwa”? Anatse Hawwa tace “Hadiza Muntari wacce was convicted sabida kidnapping yarta datayi that senate president case ish” dasauri Mrs Adebayo tace “ohh Hady we call her Hady anan, ai jiya an fitar da ita, wasu yan sanda sukazo da clearance from court they withdrew the case against her wlh she’s so lucky” sosai Hawwa ke kallon Mrs Adebayo Khaleel ne ya yafemata sabida jiya ta gayamai she will find evidence against him? Mrs Adebayo tace “why are you looking for her”? Murmushi kadan Hawwa tayi mai ciwo tace “kinsan nine nai investigating case din but well that aside nace ko kunada home address nata yar wani gari ce kinsani”? Girgiza mata kai tayi tace “no gaskiya yar Bidda ce but bamu da address nata” Shiru Hawwa tayi saikuma chan tamike tabata hannu suka gaisa tace “thank you very much” tawuce tafita.

Tunda tafito tana tafiya zuwa parking space ta hango Khaleel tsaye jikin motarta tsaye yana sanye da dogon wando da shirt dabai saka boturan sama ba, faduwa gabanta yayi akwai tracker a motarshi ne datake ja yanzu? How did he know tana nan? Daurewa tayi ta karasa ko kallo bai isheta ba tazo zata wuceshi tabude motan ya fizgota tadawo baya kaman paper azuciye Hawwa ta buge hannunshi tace “don’t touch me again! Stop touching me!” dan zaro manyan fararen idanunsa Khaleel yayi yace “someone is in a bad mood today wow!” Yadanyi dariya yana kallon yanda tahade fuska tana kallonshi yace “smile it’s Sunna!” Hararanshi tayi jin abinda yace tace “so kasan sunna” tashiga fizge hannunta yaki saki sai kawai yabude bayan motanta dan tariga tai unlocking car din da key hannunta tun dazu datazo wajen, yaturata cikin motan yashigo shima da sauri ta matsa baya tamai ihu. “Wai mehaka? Leave me alone!” Dan cute smile yamata yace “sabida kinga matar nan an saketa is that why you’re in this bad mood?” Ja idanun Hawwa sukayi takalleshi azuciye tace “even if it means me bringing down the whole world searching duk lungu da sako I will do it! I will get Evidence and I will show Baba and my entire family the kind of person you’re! Khaleel just know this and keep it at the back of your mind bazan taba zaman aure dakai ba, you’re a worthless boy da baisan darajan mata ba! You don’t value mata! You treat us like trash! And I refuse to be one of your victim”Khaleel na kallonta yadan rage murya yace “konama wasu kenamawa? Why do you hate me?” Ihu Hawwa tamai tanaji kaman ta shakesa tace “I hate you sabida you’re a piece of thrash! I hate you sabida you’re a f*ck boy! I hate you sabida you’re a playboy! I hate you sabida you think life is just about women, money and parties! Kace nikamawa dazan tsaneka?” Tadanyi shiru kadan takalleshi da masifa eyes nata tace “kasan abinda ake cema ciwon y’a mace na y’a mace ce? I hate you sabida abinda kama all those women daka wulakantar” dan tabe baki yayi yace “I don’t want them why should I keep them?” Hawwa afusace tace “you don’t want them why did you marry them and ruined their life eh Pop boy”?.

[10/6, 10:39 AM] +234 706 565 5343: EPISODE 53

Dan shiru Khaleel yayi yana kallonta ganin yanda zuciyanta ke tafarfasa, she's really angry today, and as far as he's concern he didn't ruin any girls life rather he makes their life even better and colorful, all of them and family nasu are living large yanzu, lumshe idanu yayi yabudesu kadan ya kalleta murya chan kasa yace "I can't stay 2days without having s*x!" Wani irin yammm kunnen Hawwa yayi jin abinda yafadi tadan dauke kai daga kallonshi da sauri, murya chan kasa yace "I started getting married at 24yrs, call me anything ni ba mazinaci bane Mommy na auramin su ne nayi s*x" runtse idanu Hawwa tayi da kyar tabudesu zuciyanta na radadi yanda yake magana akan mata tace "sannu Moms boy! Mata sun dawo maka toys for your selfish satisfaction eh dan gata"? Kallonta Khaleel yayi asanyaye Hawwa taji kaman zata kama da wuta ganin yanda hankalinshi kwance tace "okay nima so kake na shiga cikinsu tell me I will be your 10th wife ko 20th?" Anatse kai tsaye kuma yace "14th wife actually!" Wani zuciyane ya debi Hawwa batasan sanda tayo kanshi takama gaban riganshi ba fearlessly ta jijjigashi ranta na kuna tace "how dare you marry me Khaleel? Sabida kaga nakai 29yrs banyi aure ba is that why you took advantage of desperate state na Baba na and use the perfect timing ka aure ne eh talk?" Tayi maganan Hawaye na cika idanunta sosai tana kallon fuskanshi ta rike gaban shirt nasa gam gam, Khaleel yayi shiru yaki magana ganin ranta abace yake yau sosai cikeda bakin ciki ganin yaki magana Hawwa tace "how dare you take away the only evidence danake sa ran zan samu na nunama Baba wayekai eh? Khaleel I don't deserve you, after good 29yrs banyi aure ba clocking 30 I've been so patient cus nasan Allah will reward me for imanin danayi, why will I end up with the worst person dana sani aduniya you!? I'm too good to be your wife, you are a bad bad badddd person Khaleel I hate that kai Baba ya auramin!" Tai maganan hawaye na saukowa daga idanunta tana kallon cikin kwayan idanunsa kaman yanda yake kallonta shima, all this while batai kuka ba sabida tanasa ran she will have something to show Baba but yau da Khaleel yayi outsmarting nata sai taji duniya yamata zafi, duka takaimai a robust chest dinshi hawaye na dauka daga idanunta tace "I hate that kai Baba ya auramin! I hate you Khaleel I hate hate hate you na tsaneka! Na tsaneka" tafashe da kuka tana kaimai duka sosai akirjinshi duk yana kallonta asanyaye, cikin kuka tace "I remembered the day daka fadamin one day sainai kuka ina begging naka for mercy agaban that super market" cikin kuka har shesheka take hawaye har gemunta tace "you won! You won! You won Khaleel, I'm sorry for everything Ibrahim! I'm sorry for being rude, for insulting you calling you jobless, I'm sorry for everything dan Allah kasakeni! Please divorce me dan Allah" tashiga kuka sosai bana wasaba, bata taba sanin zata iyama Khaleel kuka hakaba, ahankali Khaleel ya lumshe idanunshi da hannu daya ya fizgota yasata ajikinshi "leave me leave me" Hawwa tai ihu amman saida yasata ya kankameta sosai tun tana hargowa hartai shiru ajikinshi tana kuka ahankali.

Lumshe idanu Khaleel yayi yana shakan cool kamshin datakeyi dayamai dadi sosai tana kuka yakai bakinshi saitin kunnenta yana matseta ajikinshi ta yanda bazata iya fitaba murya chan kasa yace "I'm glad

kinyi admitting defeat Kulu Khaleel never loose a fight! Mace bazata taba winning dina ba!" Zatai motsi yariketa gam ahankali yace "I will never divorce you Kulu! This Khaleel you hate so much saikinyi rayuwa dashi har abada!" Yadanyi dariya kadan mai sound yace "maybe da baki tsaneni ba danai letting naki go" awani irin hankali yace "and I will sex you just like yanda nakeyi da all the rest of those girl creatures, I will add you to the collection of women I slept with!" Yanda Hawwa ke fizge fizge kaman zata tashi amman yahanata fita daga jikinshi, yakara kai bakinshi wajen kunnenta yace "kinata neman evidence akaina bayan nine keda evidence akanki" yayi wani makirin murmushi yace "imagine Baba yaga video or pictures of when you were trying to rape me kina shamin baki, grabbing my shirt just like yanda kikayi dazun nan, trying to reap off my shirt and strip me naked, how will Baba feel?" Fizgo kanta Hawwa tayi daga jikinshi ta sauka gefe takalleshi da jajayen idanunshi tace "wat are you talking about? Ko zanyi raping maza aduniya trust me i will never go for national cake irinka da karabama all matan garin nan jikinka!" Shiru Khaleel yayi yana kallonta babu macen data taba gwada kalan zagin da Hawwa kemai, she just called him national cake, dan ijiyan zuciya ya sauke, wayanta dake inda take zaune yanuna mata yace "check your phone?" Dasauri Hawwa ta dauki wayan tabude, tana dubawa taga yatura mata hoto ta iMessage guda daya inda take saman kanshi bakinta akan nashi tarikemai gaban riga duka jikinsu ajike hannunta yahau rawa takalli Khaleel da sauri cus she's confuse, kanshi yadan sosa irin na iskancin nan yace "I have the video inhar u finally took off the shirt kina shamin this" yanuna mata nipples dinshi cikeda iskanci, yadan kalli saman motan kaman mai tunani yadaura yatsa abaki saikuma yacire yakalleta yace "I will just start crying to Baba ince yarshi beat me up ta turani cikin ruwa tafito dani kawai tahau kissing baki na and kikayi threatening dina kan cewa dole saina aureki, nazo nagayama Baba, Baba will easily believe me daman that crazy woman tace zaki iyama maza fyade so I'm your first victim" yakashe mata ido daya a iskance Hawwa na kallonshi hawaye na cika idanunta, Comfortably Khaleel yace "idan bakija bakin nan that talks like parrots kinyi shiru anyi bikinmu an kawomin ke gidana ba I will expose this" yanuna mata wayanta yace "family naki will lose all respect for you and zama dani dole, anyhow u look at it I'm still the winner, ko kinaso ko bakiso saikin zauna dani, don't forget you started this war with me Kulu!" Glass nashi ya warware ya sanya a idanu sannan ya kalleta yace "see you Kululuwa Yar Sanda bye" yabude kofa yafice abinshi yawuce nashi motar aka budemai brabus dinshi yazauna aka ja motan harsaida Hawwa ta daina ganinshi tafashe da kuka sosai tana kallon hoton tana mamaki what happens to her? How come is this picture photo shop ko sun bata wani abu ranan ne tunda yan kwaya ne how did she kiss this man cus batasan sanda akaiba, takai 20min tana kuka amota sannan ta tada motan tabar wajen.

**

Ijiyan zuciya Momy tasauke cikeda damuwa tana kallon Salman daya gama koramata bayani acikin office dinta hannu tasa ta zare glasses dake kan idanunta tashafa goshinta cikeda damuwa tace "why that police girl in all matan dake duniyan nan dan Allah? Ko yar india Khaleely yake bukata zan iya auromai why that girl? Akanme yake chasing nata up and down tell me the truth Salman sonta yakeyine?" Cikeda girmamawa yace "I can't say Hajiya gaskiya, but one thing is bantaba ganin Yallabai na bin mutum up and down kaman yanda yakebin yarinyar ba shi kanshi ba lallai yasani ba but he's giving her all of his attention his time and komi Ma'am" table Mom tabuga tace "that's wat I don't want, yarinyar will take

my son for granted wlh, zata wahalar min dashi Khaleely baitaba bibiyan any girl aduniyan nan ba saidai su suyita bibiyansa what is so special about tsohuwan yarinyar nan da he’s all over her eh? Hmm, u can go Salman just keep me posted whenever he sees her and wat they discuss about” gyadamata kai yayi yace yes Ma yawuce yafita.

Tashi tayi ta tsaya jikin window ta hango Khaleel din na buga ball da Noor he looks so happy haka Noor ma Mom ta sauke ijiyan zuciya, bude kofan office din nata Mom tayi tashiga another elevator dake wajen tasauka kasa tana tafiya zuwa garden da Khaleel ke buga kwallo Noor dake sanye da jersey na Liverpool looking so cute tace “Granny join us” murmushi Mommy tamata tace “continue playing Princess dina” takalli Khaleel dake wasa da kwallo abinsa kaman bai ganta ba tace “why do you keep chasing that Police girl Khaleely?” Batare daya dagokai ya kalli Mom ba yana bugama Noor kwallo yace “what is your business with my affairs Momy”? Dan shiru Mom tayi taji zafin amsan daya bata inda sabo sun saba haka yake musu magana agantale, ahankali tace “common My Leely I didn’t train you to be going after kowace kalan mace aduniya! You have everything na rayuwa babu wacce kakeso dabazaka iya samuba” daidai lokacin yabuga kwallo araga shida Noor sukahau suna jumping suna ihu yadagata yana ihu suna dariya sannan yasauke ta yace “go to your Nanny tamiki wanka” dasauri Noor tawuce tana gudu shikuma yadauki kwallon cikeda iskanci ya wurgama Mom tai baya baya kaman zata fadi sannan tarike ball din da kyar tana haki tace “Khaleely banson iskanci fa, karyewa kakeso nayi?” Khaleel ya kwashe da dariya sannan yataho inda take yabata sidehug yana daura hannunshi akafadanta cikin sangarci yace “Mom tsoro kike zan auro miki yar sanda?” Hade fuska tayi hakan yasa ya kwashe da dariya again Mom ta tsaya tana kallonshi he’s so happy this days, Khaleel yace “Mom do you think she will stop me from living my life? And enjoying myself?” Cikeda damuwa Mom tace “eh mana Khaleely girls like her sunfi karfinka” dariya yayi yace “Mommy I’m man enough to control kowace kalan mace na aura your Son is not a boy” yasaketa yawuce saikuma yadawo ashagwabe yace “Moma we will be having wedding on 23rd get ready invite all your friends, I want my side furnitures change, sannan agayara my main flat” yanuna wani arnen flat dake dayan barayin gidan dasauri Mommy tace “no Khaleel you will never leave my sight gaskiya side dinka dake cikin flat dina zaka dinga zama not bangaren chan kaji ba” wucewa yayi abinsa batare daya kulata ba yatafi sama gym dinshi yashiga yashiga yin exercise kafin daga bisani yafada shower yayi wanka yafito Sam haryazo suka tafi party abinsu.

[10/6, 10:39 AM] +234 706 565 5343: EPISODE 54

Ranan gabaki daya Hawwa jitayi batajin dadin komi, har Ramla saida taga Hawwa was not in good mood sabida yanda tai shiru batama iya magana da kyau, sai lissafi take how zata fita daga this mess? Idan yanuna video ko pictures yacema Baba tayi kokarin mai fyade duk zasu yarda ta ina kunya zai barta ta kallesu dagashi har Ammi that means everything Ni’ima said is true about her.

Washe gari tsaf ta shirya ta tafi aiki around 12 DIG yakirata tashigo office nashi murmushi yamata yace "okay Ogana gabaki daya yakirani yace nabaki leave sabida kiyi planning wedding naki da kyau an baki 60 days" zaro idanu Hawwa tayi tace "Innalillahi 60 days that's 2month, mezanyi da all this time Sir"? Dan murmushi DIG yamata yace "Hawwa have you seen abinda nafada miki jiya? Imagine danaje wajen Babanki to, wannan da Ogana ne yakira yace abaki 2months wedding leave abinda 3weeks ake bayarwa but naki is different, so zaki iya tafiya, we will see you on the wedding day in sha Allah idan kinyi inviting namu, Hawwa May Allah bless your home, Allah miki albarka, nasanki da ibada da yawan azumi Allah shine maganin komi so call on to him shine yasan wats best for you" kuka taji yana zuwan mata amman tahadiye ta gyadamai kai ta tashi ahankali tafito tana tafiya zuwa office nata wani officer yace "Miss Hawwa kinada bakuwa bamu barta tashigo nan ba tana chan" yamata pointing waiting room nasu, da mamaki tadinga tunanin waye ko wacece zatazo wajenta, dudda Ammi na hanya dan yau zata dawo amman ai baici ta iso ba tace mata by 11 zatabar gida, why is she even thinking of Ammi? Ammi bazata taba zuwa wajen aikinta ba, hanyar waiting tayi ganin Ni'ima taci gayu cikin atampa mai kyau ta yafa dan gyale ta rike handbag a hannunta yasa ta tsaya turus Ni'ima tamata murmushi kawai ta taso da gudu tazo batai wata wata ba ta rungumeta tace "Best suprise" chak Hawwa ta tsaya without hugging her back harsaida Ni'ima tadago ta kalleta tace "are you not happy to see me?" Dan girgizamata kai Hawwa tayi tace "no is not like that" dasauri Niima tace "muje office naki anata kallonmu anan" kawai takama hannun Hawwa, ahankali Hawwa tabita har zuwa office nata suka shiga idanunta ne suka sauka akan iPhone 15 pro max na Hawwa dake kan table last she check Hawwa was using Samsung S10 harya chanza mata wayane? Lallai gayen nan, abu taji ya tsaya mata arai dasauri tasaki hannun Hawwa tai wajen wayan tadauka tace "wow kin chanza waya Hawwa? Kin koma iPhone? Ni fa banson iPhone ance basu rike charge duk application saika saya? Baka iya downloading movies anyhow, komi kudi, Ke kika siya ko mijinki ya saya miki"? Karasowa Hawwa tayi ciki tazauna ahankali tace "shi ne" wani irin murmushi Ni'ima tana danne bakin ciki da zafi datakeji aranta tayi tace "awwwn lovebirds, ohh my my, Hawwa I'm happy for you Allah yaga how patient you are yabaki mai sonki, wai yaushe kuka hadu ne baki taba bani labarinsa ba, eh yaushe kuka hadu?" Baki Hawwa tabude zatai magana akai knocking kofan da sauri dukansu suka kalli kofan Abraham ne ganin Ni'ima yasa ya tsaya yace "can I see you Miss Hawwa"? Gyadamai kai tayi tace "sure" ta mike suka fice tarufe kofan dawani irin sauri Ni'ima ta danna screen din wayan ganin babu password yasa tashiga cikin wayan dasauri tace "calls" call log tashiga d only number datai magana dashi for long batai saving ba saina Ammi datai saving da Ammi hakan yasa tashiga kwashe number da she's sure Khaleel ne dan ya kikkirata bata dagawa daidai tana gama kwasa tanaji ana taba kofan da sauri tafita tarufe wayan ta ijiye kan table Hawwa ta shigo rike da Maltina ta ijiye gaban Niima, Ni'ima tace "thank you Best" Hawwa ta zauna Ni'ima tace "gist me Best ya shirye shirye? Kayan daki kayan kitchen? Na kaiki wajen wanda yamin na dakina?" Ahankali Hawwa tace "Baba da Ammi are in charge of everything bansan mesuke ba" gyadamata kai Ni'ima tayi saikuma tace "wai har yanzu kin rikeni azuciye ne? Best I'm really sorry wlh ina sonki you mean the world word to me kinji" dan lumshe idanu Hawwa tayi saita gyadamata kai tareda bude idon, Ni'ima tace "anko fa? Nafitar miki da anko?" Shiru Hawwa tayi saikuma ta gyada mata kai, murmushi Ni'ima tayi tace "thank you, can you call Baban Yaseer for me yanzu da wayan naki"? Shiru Hawwa tayi all maganganun Ammi nadawo mata ahankali tace "Ni'ima banso nakara shiga lamarinki da Baban Yaseer I promise kaina that, for licence naki nayi magana za'a samu nasara in sha Allah" murmushin karfin hali Ni'ima tayi tana danne abinda takeji azuciyanta tace "shikenan hakan ma I'm grateful after kalan abinda namiki not everyone will even help

me that much, kinada zuciya mai kyau Hawwa, thank you" gyadamata kai Hawwa tayi, daidai nan wayan Hawwa yahau ringing Ni'ima ta saci kallon screen din ganin number data kwashe ne kaman Hawwa bazata dauka ba, but ganin Ni'ima and tanaso tanunama Ni'ima she's cool with Khaleel kodan tacire tunanin Baban Yaseer da ita aranta yasa gently tadauka takai kunnenta, murya chan kasa Khaleel yace "I sent a delivery guy what's your office number"? Shiru tayi chan tace "baza'abarshi ya shigoba" dan murmushi yayi yace "no one can stop my delivery, office number Kulu" murya chan kasa tace "0040" katse wayan yayi almost 1min saiga knocking anatse Hawwa tace "come in" bude kofan akayi wani delivery guy ne rike da flowers na red roses da akai wrapping katon gaske, saikuma platter na yan gayu na different intercontinental dishes da note ajikin both of them delivery guy din yace "I'm looking for Mrs Hawwa Alhassan Ibrahim Khaleel" Ni'ima jitayi yawun bakinta yayi daci da kyar tahadiye, ahankali Hawwa ta mike ta nunamai table din zuwa yayi yafara mika mata flowers din dake kamshi sosai like Khaleel plus kamshin roses again, office din yacika da kamshi, karba tayi ta ijiye sannan yabata platter na abincin shima ta ijiye yabata note nashi tai signing sannan ya tafi, kafin Hawwa ta zauna har Ni'ima tasa hannu tadauki card dayayi note ajiki tace "love bird bari muga meya rubuta miki" dasauri kafin Hawwa tace wani abu, tace "_I know you haven't had breakfast banson matana looking skinny you are too light for my liking, eat and get chubby, cheers to starting your leave today! Sowie about yesterday with love Mijin Kulu❤️_"

Murmushin dole Ni'ima tayi ta ijiye card din, taja platter box na abincin tana budewa tace "eat mana" wow tafadi ahankali lafiyayen abinci ne aciki dat are very hot, mash potatoes da chicken wings, samosas, Pasta sai Mandi rice, ga salad ga fruits juice very cold ga sweet da cingum na mentos, kallon abincin itama Hawwa take, deep down she feels happy but then she don't wanna feel d happiness ahankali tace "ke kici idan zakici" dasauri Niima ta girgiza kai tace "a'a inacin abinci nafito" gyadamata kai Hawwa tayi saita rufe platter ta matsar gefe idanunta suka sake saika akan rose din kawai ta tsaresu da idanu Niima duk na kallonta, aranta tace "munafukar mugun son mijinta take amman tana bobboyewa, hala ma sun riga sun sadu" wayan Hawwa ya shiga ringing dasauri ta waigo ganin Khaleel ne yasa ahankali tadauki wayan takai kunne murya chan kasa Khaleel yace "have you eaten? Is the food good? Kona chanza mana Chef? Shizai dinga mana girki bayan auren mu, abincin yayi"? Shiru Hawwa tayi murya ciki ciki tace "mesa baka dafa da kanka ba"? Dan zaro idanu Khaleel yayi yace "Momy bata barina in kitchen I don't know me akayi a kitchen" murya chan kasa Hawwa tace "uhnn Moms boy" murmushi kadan Khaleel yayi yace "do you like the rose?" Kin magana Hawwa tayi, ahankali Khaleel yace "but I said sowie about yesterday" murya chan kasa Hawwa tace "sowie is not sorry" dan dariya kadan Khaleel yayi ahankali yace "wa akace tana tareda ke a office?"

[10/6, 10:39 AM] +234 706 565 5343: EPISODE 5️⃣5️⃣

Faduwa gabanta yayi jin tambayan daya mata, hakanan sai takasa magana, "answer me" yafadi da kakkausan murya still kin magana tayi sai kawai ta zare wayan daga kunnenta takatse ta ijiye takalli Ni'ima ahankali tace "zan tafi gida natashi" tashi Ni'ima tayi tace "toh nima bari natafi, bari natayaki

daukan rose din saike ki dauki platter" wani iri Hawwa taji amman saita daure ta mike tashiga hada abubuwanta tadauki car key suka fito tare ita tana rikeda platter Ni'ima na rike da rose din har zuwa inda motar Hawwa yake, Ni'ima sai kallon motar take tanaji kaman tahadiye zuciya ta mutu idanunta harsun kada sun chanza, abayan motan sukasa komi Ni'ima na kallon motan irin wannan fa ba tokunbo car Hawwa ke dashi ba no, asalin sabuwa gal ce, komi na motan ba ariga an daye mata ledaba, maida kofan bayan Hawwa tayi tarufe tace "bye" tawuce ta shiga gaba Ni'ima na tsaye tana kallonta, Hawwa taja mota tabar wajen abinta, da kyar Ni'ima ta iya wucewa zuwa wajen tata motar zuciyanta kaman an barbada busheshen barkono da danye tsabagen azaban radadi dayake mata, sai kawai ta tsaya tana kallon motan ta, motar Hawwa tada Toyota Camry ce 2006/2007 ita lokacin da Baban Yaseer yabata Camry nan na 2014 kaman zata haukace dan tafi na Hawwa kyau da tsada gata latest, but yanzu dataga motan da Hawwa keja benz datakai irin 150M sai taji ta tsani tata motar, saitaji ta rainata, wai tayaya ma rana daya Allah zai dauki miji mai bala'in kudi yabama Hawwa ne? Eh? Within a blink of an eye rayuwan Hawwa ya chanza kakap, big phone iPhone 15 pro max, ita tana fama da Samsung S21 dinta da ada takejin dadi yafi na Hawwa S10, Hawwa ce big car, ga sadaki mai tsoka, ga gwalagwalai, Hawwa ko sisi taki bata, da dane da hala yanzu Hawwa tabata like 20M from that sadaki wlh dan Hawwa bata kyashin bata abu, Hawwa is going to big house now and yaron seems to love her alot, jibi yanda yake bata gifts, ranan su diamond agogo dasu turare yau abinci da flowers masu tsinannen kamshin dadi, he's so romantic, she thought babu miji that will be as sweet and romantic as Baban Yaseer yanzu taga wanda yafisa.

Hawwa ta hadu da irin gayen kan taki fadamata har sai bayan tayi hauka? The way suke soyayya hakan nan she can swear Hawwa tadan jima da sannin gayen? Wannan dayaketa bata gifts sunyi sex ne? Hawwa is so happy she wants her to be sad, tafison taga hawaye da bakin ciki da bacin rai da damuwa akan fuskanta, wannan gayen ya shigo rayuwanta yasa Hawwa ta chanza bata damu da itaba yanzu, imagine wai ita Hawwa ke shama kamshi, what will she do yanzu? Da kyar ta lallaba tashiga motan ta tada tabar wajen tana tana tafiya akan titi tazo ta wajajen banex ta kalli masu bara dake wajen, sai kawai tayi parking motan tafito taje wajensu tace "zan baku kyautan kudi sosai amman saikun bani wayanku na tura wani sako" har rige rigen bata wayan ake, kakkarba tayi marasa kati har tana samusu ta bank dinta, sako tashiga turama number Khaleel da kusan duka number su sannan ta basu 5k suraba tawuce takoma mota tana murmushi taja abinta zuwa gida.

**

Khaleel na cikin mota tareda Sam wayanshi yayi kara daukan wayan yayi yaga messages guda 5 from different numbers hardly unknown ke kiranshi ma talk more of sako, kaman bazai budeba saikuma yabude daya.

"_Hawwa is a whore! Tsohuwan karuwa ce she sleeps with everyman dayake zuwa yace yana sonta saisa suke guduwa basa aurenta sabida tabasu abinda suke nema_"

Chak Khaleel ya tsaya yana kallon messege din to be very very honest he doesn't care idan Hawwa sleeps around or not cus yasan tun zamanin da wato old days aka daina samin virgins, konji is real babu yanda za'ayi yataso maka baka nemi wanda you will sleep with ba so what ai d'ane tayi, baida right to judge her life is not easy takai this years 29 without a man, shi tun yana 24 yafara ai, but dudda haka saiyaji still zuciyanshi namai wani iri sai kawai ya ijiye wayan da sauri without opening sauran messages din ahankali yace "park the car" Dasauri Sam yace "lafiya? We are not there yet" dan murmushi Khaleel yamai yace "just give me a moment" fita yayi daga motan yafara tafiya zuwa chan gefen titi baitaba sani akwai randa za'a gayamai wata yar iska ce harma yaji abun yadameshi ba, ko yadingajin ciwo aransa ba, duk sai yaji wani iri, who even send the message? What if is Hawwa? He don't think she will ever defame kanta dudda yasan batason auren su but Hawwa is someone that value self respect and image nata, ko kadan batason compromising self respect and imagine nata saisa he even use that picture and threaten her with it, cus yasan she will not want him to expose that koda ba gaskiya bane dan she values her self respect, juyowa yayi yakalli Salman daya fito daga motan yana kallonsa da hannu yama Salman alamu daya daukomai wayansa amota daukowa yayi yazo wajen yakawomai dasauri ya karba yabude second message din.

"_Hawwa babe din boss dinta ne DIG she slept with him in order ya dauketa yasata a task force din nan dan she was an ordinary police girl before without any star_"

Sai another message. "_Officer Hawwa sleep with yaran office example Abraham data girmeshi da shekaru slept with Hawwa countless times_",

Yanda zuciyan Khaleel ke bugawa kasa cigaba da bude sauran messages din yayi ya manna ma Salman wayan a kirjinshi yace "track those numbers all of them for me, track them! I need information uuughhhhh!" Ya dunkule hannu yayi punching air yawuce fiuuuu yatafi mota ya shiga da kanshi yarufo da mahaukacin karfi akaja motan Sam yace "lafiya are you okay"? Lumshe idanu yayi yaki magana har sukakai party saukowa yana shiga yadauki about 5 shots na tequila yana sha Sam yace "Lee are you okay? Why are you drinking like that" ko kallonshi baiyiba shaye shayen dayahau yi saida yabama duka abokanshi tsoro saida yayı total out sannan Sam da Moh suka kaishi sama aka kwantar dashi agado Moh yace "kasan what's wrong with him"? Girgixamai kai yayi suka wuce suka fita daga dakin aka barshi warwas agado.

[10/6, 10:39 AM] +234 706 565 5343: EPISODE 56

Washegari Khaleel yafarka adakinsa da kyar ya lallaba yaje yayi salla wuraren 9, ko wanka baiyiba yafito yasauko kasa Mommy na falo tace "good morning Son" ko kallonta baiyiba Noor ta taho wajenshi da gudu tace "Daddy" kanta yashafa kadan yace "go to grandma I'm coming Noor" yafice idanunshi sunyi ja duk sun nuna alamun bacci, yayi waje yana kallon Salman daya taho da sauri Khaleel yace "ya?" Salman

yace “we tracked the numbers duka numbers din beggars ne dake hanyar banex, da kyar bayan nabasu kudi suka iya sanar dani wata mace ce tazo tabasu 5k tayi amfani da wayansu” dasauri Khaleel yace “did you ask them description nata?” Salman yace “yeah wai batada tsawo sosai she’s very fair and da Toyota tazo” shiru Khaleel yayi kaman mai tunani, kawai yawuce wajen motar sa Salman yabiyosa ya shiga driver ma yashiga sukabar gidan, ahankali cikin muryan gajiya da bacin rai yace “my wife’s house” jan motan sukayi  har zuwa unguwan su Hawwa.

Baba na kofar gida azaune da aswaki a bakinsa ya hango mota yasan Khaleel ne kawai sai yafara murmushi kafin ma abudemai Khaleel yabude da kanshi yafito Baba ya tsareshi da idanu ganin idanunshi adan kumbure hakama fuskanshi dasauri Baba yataso shima Khaleel yawuce wajen Baba kafin yayi magana har Baba yakai hannunsa kan fuskanshi cikeda so yace “bakada lafiya ne Ibrahima”?Baba Khaleel ya kalla dan ranshi abace yake yayi shiru yakasa magana sai dan huci da yasauke Baba sai kawai hankalinsa yatashi yace “meya sameka? Tell me”? Dan ijiyan zuciya yasauke yajuyo yakalli Salman da hannu yamai alamu yakawomai wayanshi wayan aka kawomai muryan Khaleel ba dadi yanunama Baba wayanshi yace “Baba wasu sakonni aka turamin marasa dadi bazan iya karanta maka ba kaima, nasa ammin tracking number” yadanyi shiru Baba da gabanshi ke faduwa yace “ina jinka gayamin menene ke faruwa”? Cikeda jin zafi Khaleel yace “Baba matana ta batamin rai sosai, ina kyautata zaton har yanzu tana tareda mahaukaciyan nan, so nazo na ganta ne”

Dudda Baba baiga sakon ba but ayanda yaga Khaleel yasan Ni’ima tayi wani abu ranshi inyayi dubu yabaci tsabagen bacin rai yace “muje ka shiga gidan kacimata mutunci ba anan waje zan kiramaka itaba, ai gidana nakane ban maka iyaka da ko’ina acikin gidannan ba, muje” Baba yayi gaba Khaleel yabishi abaya suka shiga cikin gidan ko’ina a gyare ta buga sallama gaban dakin Hawwa, Ammi ta amsa yace “da mijin Hawwa nazo Zainabu” Hawwa dake zaune daga ita sai dan rigan bacci tana danna wayanta dasauri tadauki hijabi tasaka dark blue har kasa, ita dama Ammi da hijabi ajikinta Ramla kuma na kitchen tana aiki dasauri Ammi ta tashi da fara’a tace “bismillah bismillah kushigo” shigowa Baba yayi Khaleel biyeda shi abaya, kan Khaleel na kasa yace “ina kwana Mom” “muntashi lpy Khaleel” ahankali Baba yace “biyoni Ammi” binshi Ammi tayi suka fice daga dakin tareda maido musu da kofan suka rufe, Khaleel yazuba hannu a pocket nashi yana kallon Hawwa dako dagokai batayi ta kalli inda yakeba, kaman ma batasan da mutum awajen ba, Babu wasa kan fuskanshi rai abace yace “wacece ke tareda ke jiya a office?” Batare da Hawwa ta kalleshi ba tace “da wanda nake tare, ko wanda nai magana, ko wanda nagani a office is none of your damn business” ran Khaleel abace ya daka mata tsawa da saida dakin ya amsa. “Nace dawa kike tare jiya an office!”? Dagokai Hawwa tayi adan tsorace sabida yanda yayi mata tsawa ta tabbata anji a tsakar gidan, tashi tayi daga gadon ta taho inda yake dasauri dan bataso su Ammi suji tanamai ihu suhau mata fada akanshi, hakan yasa tace “who do you think you are kanamin ihu aka?” Ran Khaleel abace yanunata da hannu yace “dawa kike tare an office jiya?” “My friend!” Hawwa ta amsa kai tsaye ganin yadameta da tambayan, cikeda jin haushi tace “I was with Ni’ima me akayi? Sabida an auramin kai saina tambayeka kafin naga kawata konai magana da kawata”? Wani irin fizgota Khaleel yayi yakai hannunshi

zuwa wuyanta ranshi abace yace “what is so special about that witch of a woman da kin kasa hakura da ita? Are you a lesbian!? Are you really into girls?”

Ja idanun Hawwa suka soma yi tafara dukan hannunshi hakan yasa yasaki wuyanta tadanyi tari kadan sannan ta kalleshi tace “da aurenka gwara zama da Ni’ima! At least ita bata living wayward life irin naka!”Radadi zuciyan Khaleel yafara sai kawai yakara fizgo Hawwa yakama kafadunta ya matse yana kallon cikin idanunta zuciya yakaimai wuya da kishi kai da komi ma ganin yanda Hawwa ke son Ni’ima yace “idan nakara ganin ki da yarinyar nan i will killl her! I will ruin her life! I will make her life a living hell you know me so well to know duk abinda nakeso nayi sainayi, stay away from that witch evil vile woman inba hakaba saina kasheta!”

[10/6, 10:39 AM] +234 706 565 5343: EPISODE 57

